يَعۡتَذِرُونَ إِلَيۡكُمۡ إِذَا رَجَعۡتُمۡ إِلَيۡهِمۡۚ قُل لَّا تَعۡتَذِرُواْ
لَن نُّؤۡمِنَ لَكُمۡ قَدۡ نَبَّأَنَا ٱللَّهُ مِنۡ أَخۡبَارِكُمۡۚ وَسَيَرَى
ٱللَّهُ عَمَلَكُمۡ وَرَسُولُهُۥ ثُمَّ تُرَدُّونَ إِلَىٰ عَٰلِمِ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٩٤ سَيَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ
لَكُمۡ إِذَا ٱنقَلَبۡتُمۡ إِلَيۡهِمۡ لِتُعۡرِضُواْ عَنۡهُمۡۖ فَأَعۡرِضُواْ
عَنۡهُمۡۖ إِنَّهُمۡ رِجۡسٞۖ وَمَأۡوَىٰهُمۡ جَهَنَّمُ جَزَآءَۢ بِمَا كَانُواْ
يَكۡسِبُونَ ٩٥ يَحۡلِفُونَ لَكُمۡ لِتَرۡضَوۡاْ عَنۡهُمۡۖ فَإِن
تَرۡضَوۡاْ عَنۡهُمۡ فَإِنَّ ٱللَّهَ لَا يَرۡضَىٰ عَنِ ٱلۡقَوۡمِ ٱلۡفَٰسِقِينَ
٩٦ ٱلۡأَعۡرَابُ أَشَدُّ كُفۡرٗا وَنِفَاقٗا وَأَجۡدَرُ أَلَّا يَعۡلَمُواْ حُدُودَ
مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ عَلَىٰ رَسُولِهِۦۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٩٧ وَمِنَ
ٱلۡأَعۡرَابِ مَن يَتَّخِذُ مَا يُنفِقُ مَغۡرَمٗا وَيَتَرَبَّصُ بِكُمُ
ٱلدَّوَآئِرَۚ عَلَيۡهِمۡ دَآئِرَةُ ٱلسَّوۡءِۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ٩٨ وَمِنَ
ٱلۡأَعۡرَابِ مَن يُؤۡمِنُ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَيَتَّخِذُ مَا يُنفِقُ
قُرُبَٰتٍ عِندَ ٱللَّهِ وَصَلَوَٰتِ ٱلرَّسُولِۚ أَلَآ إِنَّهَا قُرۡبَةٞ لَّهُمۡۚ
سَيُدۡخِلُهُمُ ٱللَّهُ فِي رَحۡمَتِهِۦٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٩٩



**(94) Munafikan da suka qi zuwa jihadi za su bayar da uzurori masu rauni ga musulmi yayin da suka dawo daga jihadi, don haka sai Allah ya fuskantar da Annabinsa da muminai irin martanin da zasu ba su, na cewa: "Kar ku kawo uzuri da uzurorin qarya, ba zamu gaskata komai cikin abin da zaku gaya mana ba, Allah ya riga ya sanar da mu wani abu daga cikin abin da ke zukatanku. Kuma da sannu Allah da Manzonsa zasu gani, shin za ku tuba, Allah ya karvi tubanku, ko zaku ci gaba da munafincinku?. Qarshe dai za a komar da ku ne zuwa ga Allah wanda ya san komai, sai ya baku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa, ya saka muku a kansa. Don haka, ku gaggauta tuba da aiki nagari".**

**(95) Waxannan da suka qi zuwa Jihadi, za su rantse muku da Allah idan kun dawo inda suke - Ku Muminai -, domin su qarfafa uzurorinsu na qarya, saboda kar ku zarge su, ku tsawata musu. To ku qyale su, ku fita daga harkarsu, kuna masu fushi da qaurace musu. Haqiqa su najasa ne masu munanan zukata, kuma Jahannama ce makomarsu da za su tabbata a cikinta ranar alkiyama, sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa na munafinci da savo.**

**(96) Waxannan masu qin zuwa Jihadi za su rantse muku ne, ya ku muminai, wai domin ku yarda da su, ku karvi uzurinsu. To kar ku yarda da su, domin in kun yarda da su, to kun savawa Ubangijinku, domin shi baya yarda da masu sava biyayya a gare shi, ta hanyar karfirci da munafinci. Saboda haka, ya ku musulmi, ku kiyayi yarda da wanda Allah baya yarda da shi!. (97) Mutanen qauye idan suka kafirce ko suka yi munafinci, to kafircinsu ya fi tsanani a kan kafircin mutanen birni, haka munafincinsu ya fi nasu tsanani. Kuma su ne suka fi cancanta da jahiltar addini, da rashin sanin farillai da sunnoni da iyakokin hukunce-hukuncen da Allah ya saukar wa Manzonsa, saboda abin da suke kai na wauta da kaushin hali da qarancin cuxanya da jama'a. Allah kuma mai cikakakken sani ne na halayensu, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma shi mai hikima ne cikin tsarinsa da shari'arsa.**

**(98) Akwai daga cikin munafikai mazauna qauye waxanda suke qudurta cewa abin da suke ciyarwa na dukiya domin xaukaka kalmar Allah hasara ne da haraji a kansu, domin suna riya cewa ba za a basu lada ba in sun ciyar, kuma Allah ba zai musu uquba ba in sun kame daga ciyarwar, amma duk da haka suna ciyarwa xin a wasu lokutan domin riya da kare kai. Kuma suna jiran wani sharri ya faxa muku – ku taron muminai- don su huta da ku. Allah ya san abin da suke fatan ya afkawa muminai na sharri da juyawar zamani a kansu, ya sa mummunan qarshe ya koma kansu, ba akan muminai ba!. Allah yana jin abin da suke faxa, kuma yana sane da abin da suke voyewa a cikin zukatansu. (99) Amma kuma akwai a cikin mazauna qauye waxanda suke yin imani da Allah da ranar lahira, suna xaukar abin da suke ciyarwa na dukiya a kan tafarkin Allah a matsayin abin da suke neman kusanci da shi zuwa ga Allah, kuma a matsayin hanyar neman rabauta da addu'ar Manzon Allah (S.A.W) da nema musu gafara daga gare shi. Haka lamarin yake! Lallai ciyarwarsu a kan tafarkin Allah da addu'ar da Manzon Allah zai musu, abubuwa ne waxanda zasu kusantar da su zuwa ga Allah. Zasu samu ladansu a wajen Allah, ta hanyar shigar da su cikin rahamarsa mai yalwa, wacce ta qunshi gafararsa da Aljannarsa. Haqiqa Allah mai gafara ne ga wanda ya tuba cikin bayinsa, mai jinqai a gare su.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Fagen aiki da sauke nauyin da shari'a ta xorawa mutum, shi ne mafi girman fagen da ake gane qaryar munafikai . 2 - Qauyawa idan sun kafirta to sun fi 'yan birni tsananin kafirci da munafinci saboda tasirin yanayi a kansu. 3 - Kwaxaitarwa akan ciyarwa saboda Allah tare da tsarkake niyya, da bayanin girman ladan yin hakan. 4 - Falalar ilimi da bayanin cewa maras ilimi shi yafi kusa da kuskure.**

وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلۡأَوَّلُونَ مِنَ ٱلۡمُهَٰجِرِينَ وَٱلۡأَنصَارِ وَٱلَّذِينَ
ٱتَّبَعُوهُم بِإِحۡسَٰنٖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُ وَأَعَدَّ
لَهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي تَحۡتَهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۚ
ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١٠٠ وَمِمَّنۡ حَوۡلَكُم مِّنَ ٱلۡأَعۡرَابِ
مُنَٰفِقُونَۖ وَمِنۡ أَهۡلِ ٱلۡمَدِينَةِ مَرَدُواْ عَلَى ٱلنِّفَاقِ لَا تَعۡلَمُهُمۡۖ
نَحۡنُ نَعۡلَمُهُمۡۚ سَنُعَذِّبُهُم مَّرَّتَيۡنِ ثُمَّ يُرَدُّونَ إِلَىٰ عَذَابٍ
عَظِيمٖ ١٠١ وَءَاخَرُونَ ٱعۡتَرَفُواْ بِذُنُوبِهِمۡ خَلَطُواْ عَمَلٗا صَٰلِحٗا
وَءَاخَرَ سَيِّئًا عَسَى ٱللَّهُ أَن يَتُوبَ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٌ
١٠٢ خُذۡ مِنۡ أَمۡوَٰلِهِمۡ صَدَقَةٗ تُطَهِّرُهُمۡ وَتُزَكِّيهِم بِهَا وَصَلِّ عَلَيۡهِمۡۖ
إِنَّ صَلَوٰتَكَ سَكَنٞ لَّهُمۡۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ١٠٣ أَلَمۡ يَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ
ٱللَّهَ هُوَ يَقۡبَلُ ٱلتَّوۡبَةَ عَنۡ عِبَادِهِۦ وَيَأۡخُذُ ٱلصَّدَقَٰتِ وَأَنَّ
ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ١٠٤ وَقُلِ ٱعۡمَلُواْ فَسَيَرَى ٱللَّهُ عَمَلَكُمۡ
وَرَسُولُهُۥ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۖ وَسَتُرَدُّونَ إِلَىٰ عَٰلِمِ ٱلۡغَيۡبِ وَٱلشَّهَٰدَةِ
فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ١٠٥ وَءَاخَرُونَ مُرۡجَوۡنَ لِأَمۡرِ ٱللَّهِ
إِمَّا يُعَذِّبُهُمۡ وَإِمَّا يَتُوبُ عَلَيۡهِمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ١٠٦



**(100) Waxanda suka riga kowa yin imani da farko, cikin Muhajirai (Wato mutanen Makkah) waxanda suka yi hijira daga gidajensu da qasashensu zuwa ga Allah, da Al-ansar (Wato mutanen Madinah), waxanda suka taimaki Annabin Allah (S.A.W) da waxanda suka biyo bayan Muhajirai da Al-ansar xin da suka riga kowa yin imani da kyautatawa, a cikin aqida da maganganu da ayyuka, Allah ya yarda da su, ya karvi ayyukan xa'arsu, su ma sun yarda da shi, saboda abin da ya basu na lada mai girma. Kuma ya yi musu tanadin Aljannatai, waxanda qoramu suke gudana a qarqashin gine-ginensu, zasu zauna a ciki, zama na har abada. Wannan sakamakon shi ne babban rabo.**

**(101) Akwai munafikai a cikin qauyawa mazauna kusa da garin Madinah, haka nan ma akwai munafukai cikin mutanen Madinah, sun kafu a cikin munafinci, sun tabbata a kansa, baka san su ba ya kai wannan Manzo, Amma Allah ya san su, kuma da sannu zai musu azaba sau biyu: ta farko a duniya, ta hanyar fallasa munafincinsu da kashe su, da kama su a wurin yaqi, ta biyu kuma a lahira ta hanyar azabar kabari, sannan za a mayar da su zuwa ga azaba mai girma a can qasan wuta a ranar alqiyama.**

**(102) A cikin mutanen Madinah akwai wasu mutanen da basu je yaqi ba, ba tare da wani uzuri ba, kuma sun tabbatar da kansu ba su da wani uzuri, ba su kuma bayar da uzurin qarya ba, sun cakuxa kyawawan ayyukansu da suka gabata na tsayuwa akan biyayyar Allah, da riqo da shari'arsa, da jihadi a kan tafarkinsa, sun cakuxa su da mummunan aiki, suna fatan Allah ya karvi tubansu, ya yafe musu. Haqiqa Allah mai yawan karvar tuba ne, ga wanda ya tuba cikin bayinsa, kuma mai yawan jinqai ne a gare su. (103) Ya kai wannan Manzo, ka karvi zakkah daga cikin dukiyoyinsu, don ka tsarkake su da ita daga dattin savo da laifuka, kuma kyawawan ayyukansu su qaru da ita, kuma ka yi musu addu'a bayan ka karve ta daga gare su. Haqiqa addu'arka rahama ce da nutsuwa a gare su. Allah mai jin addu'arka ne, kuma mai cikakken sani a kan ayyukansu da niyyoyinsu. (104) Waxanda suka qi zuwa jihadi, da waxanda suka tuba zuwa ga Allah, su sani cewa, Allah shi yake karvar tuban bayinsa, kuma shi yake karvar sadakarsu, amma ya wadatu daga gare ta, yana ba mai yin sadaka ladan sadakarsa. Kuma Shi mai yawan karvar tuba ne ga duk wanda ya tuba cikin bayinsa, mai jinqai ne a gare su. (105) Kuma ya kai wannan Manzo, ka faxawa waxanda suka qi zuwa jihadi, da waxanda suka tuba daga laifinsu cewa: Ku gyara varnar abin da ya wuce, ku tsarkake ayyukanku saboda Allah, ku aikata abin da Allah zai yarda da shi. Da sannu Allah da Manzonsa da muminai zasu ga ayyukanku, sannan a mayar da ku, ranar alqiyama zuwa ga Ubangijinku, wanda ya san komai, ya san abin da kuke voyewa, da abin da kuke bayyanawa, sai ya baku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa a duniya, ya saka muku a kan hakan. (106) Daga cikin waxanda basu je yaqin Tabuka ba, akwai wasu mutanen da basu da uzuri, don haka aka jinkirta lamarinsu zuwa ga hukuncin Allah da abin da zai zartar, Allah zai hukunta abin da ya ga dama a kansu, ko dai ya yi musu azaba in basu tuba ba, , ko ya karvi tubansu in sun tuba. Allah ya san wanda ya cancanci ya yi masa uquba, da wanda ya cancanci a yi masa afuwa, kuma shi mai hikima ne a cikin shari'arsa da tsarinsa. Waxanda aka jinkirta lamarinsu, aka ce su je sai Allah ya yi hukunci, su ne: Muraratu xan Ar-Rabi'u, Ka'abu xan Maliku, da Hilalu xan Umayya.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Fifikon gaggawa zuwa ga imani da yin hijira a kan tafarkin Allah, da taimakon addini da bin tafarkin magabata na qwarai. 2 - Kaxaituwar Allah da sanin gaibu, don haka babu wanda ya san abin da ke cikin zukata sai Allah. 3 - Fatan da muminai masu savo suke yi na samun gafarar Allah, idan har sun tuba, sun gyara ayyukansu. 4 - Wajabcin bada zakkah, da bayanin falalarta da tasirinta wajen havaka dukiya da tsarkake zukata daga rowa da sauran cutukan zuciya.**

وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مَسۡجِدٗا ضِرَارٗا وَكُفۡرٗا وَتَفۡرِيقَۢا بَيۡنَ
ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَإِرۡصَادٗا لِّمَنۡ حَارَبَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ مِن قَبۡلُۚ
وَلَيَحۡلِفُنَّ إِنۡ أَرَدۡنَآ إِلَّا ٱلۡحُسۡنَىٰۖ وَٱللَّهُ يَشۡهَدُ إِنَّهُمۡ
لَكَٰذِبُونَ ١٠٧ لَا تَقُمۡ فِيهِ أَبَدٗاۚ لَّمَسۡجِدٌ أُسِّسَ عَلَى ٱلتَّقۡوَىٰ
مِنۡ أَوَّلِ يَوۡمٍ أَحَقُّ أَن تَقُومَ فِيهِۚ فِيهِ رِجَالٞ يُحِبُّونَ أَن
يَتَطَهَّرُواْۚ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُطَّهِّرِينَ ١٠٨ أَفَمَنۡ أَسَّسَ بُنۡيَٰنَهُۥ
عَلَىٰ تَقۡوَىٰ مِنَ ٱللَّهِ وَرِضۡوَٰنٍ خَيۡرٌ أَم مَّنۡ أَسَّسَ بُنۡيَٰنَهُۥ
عَلَىٰ شَفَا جُرُفٍ هَارٖ فَٱنۡهَارَ بِهِۦ فِي نَارِ جَهَنَّمَۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي
ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٠٩ لَا يَزَالُ بُنۡيَٰنُهُمُ ٱلَّذِي بَنَوۡاْ رِيبَةٗ
فِي قُلُوبِهِمۡ إِلَّآ أَن تَقَطَّعَ قُلُوبُهُمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ
١١٠ ۞ إِنَّ ٱللَّهَ ٱشۡتَرَىٰ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ أَنفُسَهُمۡ وَأَمۡوَٰلَهُم ربع الحزب ٢١
بِأَنَّ لَهُمُ ٱلۡجَنَّةَۚ يُقَٰتِلُونَ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَيَقۡتُلُونَ
وَيُقۡتَلُونَۖ وَعۡدًا عَلَيۡهِ حَقّٗا فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَٱلۡإِنجِيلِ
وَٱلۡقُرۡءَانِۚ وَمَنۡ أَوۡفَىٰ بِعَهۡدِهِۦ مِنَ ٱللَّهِۚ فَٱسۡتَبۡشِرُواْ
بِبَيۡعِكُمُ ٱلَّذِي بَايَعۡتُم بِهِۦۚ وَذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ١١١



107 Daga cikin munafikai akwai waxanda suka gina masallaci ba don xa'a ga Allah ba, sai don cutar da musulmai, da taimakawa kafirci ta hanyar qarfafa munafikai, da son rarraba kan muminai, da tanadi da bada mafaka ga wanda ya yaqi Allah da manzonsa tun kafin a gina masallacin. Waxannan munafikai za su rantse muku da Allah cewa: “Bamu yi nufin komai ba face sauwaqa wa Musulmai”. Allah ya shaida cewa: Tabbas wallahi qarya suke cikin wannan da'awar.

108 Masallaci irin wannan, - Ya kai wannan Annabi- kar ka amsa gayyatar munafikai da suka yi maka na yin sallah a cikinsa. Haqiqa masallacin Quba wanda aka kafa shi tun farkon kafawa a kan tsoron Allah, shi yafi dacewa ka yi sallah a cikinsa, sama da wannan wanda aka kafa a kan kafirci. A cikin masallacin Quba akwai mutane masu son su tsarkake kawunansu da ruwa daga kari da qazanta, kuma su tsarkake kawunansu da tuba da istigfari daga zunubai. Allah yana son masu tsarkake kawunansu daga kari da qazanta da zunubai.

109 Shin wanda ya xora ginin sa a kan tsoron Allah, ta hanyar bin umarninsa da nisantar haninsa, kuma akan yardar Allah, ta hanyar yawaita ayyukan xa'a, shin zai yi daidai da wanda ya gina masallaci domin cutar da Musulmi, da qarfafa kafirci da raba kan musulmi?. Ba zasu tava zama daidai ba har abada!. Na farkon ginin sa mai qarfi ne, dunqulalle, ba a tsoron faxuwarsa. Xayan kuwa misalinsa kamar wanda ya yi gini ne a gefen rami, sai ya rushe ya rufta, ya faxa ramin Jahannama. Allah baya datar da mutanen da suke azzalumai ta hanyar kafirci da munafinci da waninsu.

110 Masallacinsu da suka gina don cutarwa ba zai gushe ba yana mai zamar musu shakka da tabbataccen munafinci a zukatansu, har zuwa lokacin da zukatansu zasu tsintsinke a sakamakon mutuwa ko kisa da takobi. Allah masanin ayyukan bayinsa ne, kuma mai hikima ne cikin abin da yake hukuntawa na sakamako a kan alheri ko sharri.
Bayan Allah ya fallasa ababuwan kunyar munafikan da suka qi zuwa jihadi, sai ya ambaci sakamakon masu yin jihadi dominsa. Ya ce:

111 Haqiqa Allah ya sayi rayukan muminai daga wurinsu, - duk da cewa mallakarsa ne - amma saboda falalarsa sai ya saye su da farashi mai tsada, shi ne Aljanna. Saboda yadda suke yaqar kafirai don kalmar Allah ta zama a sama, don haka sai su kashe kafirai, suma kafirai su kashe su. Allah ya yi musu alqawari na gaskiya, a cikin Attaura, littafin Annabi Musa (S.A.W), da Injila littafin Annabi Isa (S.A.W), da Alqur'ani, littafin Annabi Muhammadu (S.A.W). Babu wada yafi cika alkawarinsa fiye da Allah Maxaukakin Sarki. Don haka ku yi farin ciki da albishir –Ya ku muminai- ku yi farin ciki da wannan ciniki da kuka qulla shi tare da Allah, haqiqa kun ci riba mai girman gaske a cikinsa. Kuma wannan ciniki shi ne babban rabo.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Soyayyar Allah ta tabbata ga masu tsarkake kawunansu daga najasar jiki da ta ruhi.

2 - Wanda ya yi aiki, yayi nufin Allah da aikin, to wannan aikin shi ne wanda zai wanzu, kuma ma'abocinsa yayi farin ciki da shi. Mai wannan aikin ba zai yi daidai da wanda ya yi nufin taimakon kafirci da yaqar musulmi da aikinsa ba, kuma wannan aikin shi ne aikin da zai gushe, ma'abocinsa ya tave saboda shi.

3 - Shar'anta jihadi da kwaxaitarwa a kansa abu ne da ya kasance a cikin addinai da suka zo kafin Musulunci.

4 - Duk yanayin da zai jawo rabuwar kai tsakanin muminai, to yana cikin savon da ya wajaba a bari, kuma a kawar da shi, Kamar yadda duk yanayin da zai jawo haxin kan muminai da zaman lafiyansu to dole ne abi wannan yanayin, ayi umarni da shi, a kwaxaitar a kansa.

ٱلتَّٰٓئِبُونَ ٱلۡعَٰبِدُونَ ٱلۡحَٰمِدُونَ ٱلسَّٰٓئِحُونَ
ٱلرَّٰكِعُونَ ٱلسَّٰجِدُونَ ٱلۡأٓمِرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ
وَٱلنَّاهُونَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَٱلۡحَٰفِظُونَ لِحُدُودِ ٱللَّهِۗ
وَبَشِّرِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١١٢ مَا كَانَ لِلنَّبِيِّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ
أَن يَسۡتَغۡفِرُواْ لِلۡمُشۡرِكِينَ وَلَوۡ كَانُوٓاْ أُوْلِي قُرۡبَىٰ
مِنۢ بَعۡدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمۡ أَنَّهُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَحِيمِ ١١٣ وَمَا
كَانَ ٱسۡتِغۡفَارُ إِبۡرَٰهِيمَ لِأَبِيهِ إِلَّا عَن مَّوۡعِدَةٖ وَعَدَهَآ
إِيَّاهُ فَلَمَّا تَبَيَّنَ لَهُۥٓ أَنَّهُۥ عَدُوّٞ لِّلَّهِ تَبَرَّأَ مِنۡهُۚ إِنَّ إِبۡرَٰهِيمَ
لَأَوَّٰهٌ حَلِيمٞ ١١٤ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيُضِلَّ قَوۡمَۢا بَعۡدَ إِذۡ
هَدَىٰهُمۡ حَتَّىٰ يُبَيِّنَ لَهُم مَّا يَتَّقُونَۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ
عَلِيمٌ ١١٥ إِنَّ ٱللَّهَ لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ يُحۡيِۦ
وَيُمِيتُۚ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٖ ١١٦
لَّقَد تَّابَ ٱللَّهُ عَلَى ٱلنَّبِيِّ وَٱلۡمُهَٰجِرِينَ وَٱلۡأَنصَارِ ٱلَّذِينَ
ٱتَّبَعُوهُ فِي سَاعَةِ ٱلۡعُسۡرَةِ مِنۢ بَعۡدِ مَا كَادَ يَزِيغُ قُلُوبُ
فَرِيقٖ مِّنۡهُمۡ ثُمَّ تَابَ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّهُۥ بِهِمۡ رَءُوفٞ رَّحِيمٞ ١١٧



(112) **Wanxanda suka samu wannan sakamako su ne: Masu barin abin da Allah yake fushi da shi ne zuwa ga abin da yake so, kuma ya yarda da shi, kuma suna qasqantar da kansu don tsoron Allah da tawali'u, don haka suka yi qoqari wajen biyayya ga Allah. Masu godiya ga Ubangijinsu a kowane hali, masu azumi, masu yin sallah, masu umarni da abin da Allah ya yi umarni da shi, ko Manzonsa ya yi umarni da shi, masu hana yin abin da Allah ya hana, ko Annabinsa ya hana, masu kiyaye umarnin Allah ta hanyar biyyayya, da nisantar abin da ya hana. Ya kai wannan Manzo, ka yi wa muminai masu waxannan siffofin albishir da abin da zai faranta musu rai a duniya da lahira.**

(113) **Bai dace ba ga Annabi da muminai su nemawa mushirikai gafarar Allah, koda kuwa 'yan 'uwansu ne na kusa, bayan ta bayyana gare su cewa, su 'yan wuta ne, saboda sun mutu a kan shirka.**

(114) **Neman gafarar da Annabi Ibrahim ya yi wa babansa, ya kasance ne kawai saboda alqawarinsa da ya yi masa, cewa lallai zai nema masa gafara a wurin Allah, don kwaxayin ko zai musulunta. Amma yayin da ya bayyana ga Annabi Ibrahim cewa, babansa maqiyin Allah ne saboda rashin amfani nasiha a gare shi, ko saboda ya gane ta hanyar wahayi zai mutu kafiri, sai ya baranta daga gare shi. Neman gafarar da yi masa ya yi ne a kan ijtihadi, ba savawa hukuncin da Allah ya yi masa wahayinsa ba ne. Haqiqa Annabi Ibrahim (S.A.W) mai yawan qanqan da kai ne zuwa ga Allah, mai yawan yafiya da kawar da kai daga mutanen da suke azzalumai.**

(115) **Allah ba zai yi wa mutane hukunci da vata ba, bayan ya datar dasu zuwa ga hanyar shiriya, har sai ya bayyana musu abubuwan da suke haramun, waxanda yake wajibi su nisance su, idan sun aikata abin da ya haramta musu, bayan ya bayyana musu haramcinsa, sannan sai ya yi musu hukunci da vata. Haqiqa Allah masani ne a kan komai da komai, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma tabbas ya sanar da ku abin da baku sani ba.**

(116) **Haqiqa Allah shi yake da mulkin sammai da qassai , ba shi da abokin tarayya a cikinsu, babu wani abin da yake vuya a gare shi, shi yake raya wanda ya ga dama, ya kashe wanda ya ga dama, baku da wani koma bayan Allah wanda zai jivinci lamarinku, kuma baku da wani mataimaki wanda zai kare muku mummuna, ko ya taimake ku akan abokin gabarku.**

(117) **Haqiqa Allah ya karvi tuban Annabi Muhammadu (S.A.W) yayin da ya yi wa munafikai izinin zama a gida ba sai sun je yaqin Tabuka ba, kuma ya karvi tuban Muhajirai da Al-ansar waxanda ba su zauna ba, sun bi Annabi (S.A.W) zuwa yaqin Tabuka, duk da tsananin zafi da qarancin abin hannu, da qarfin abokan gaba, bayan saura qiris zukatan sashe daga cikinsu su karkata, su himmatu da rashin zuwa yaqin, saboda yanayin da suke ciki na tsananin wahala, Amma sai Allah ya yi musu dace na tabbatuwa da fitowa zuwa wajen yaqin, Ya karvi tubansu. Haqiqa Allah mai rangwame ne da jin qai a gare su. Daga cikin jinqansa ne ya datar da su zuwa yin tuba, kuma ya karvi tuban daga gare su.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Vacin kafa hujja a kan halaccin nemawa mushrikai gafara da aikin Annabi Ibrahim (S.A.W).**
**2 - Zunubi da savo su ne sababin musifu da tavewa da rashin dacewa.**
**3 - Allah shi ne mamallakin mulki, Shi ne majivincin lamarinmu, bamu da wani mai jivintar lamari ko mai bayar da taimako koma bayansa.**
**4 - Bayanin falalar sahabban Annabi (S.A.W) akan sauran mutane.**

وَعَلَى ٱلثَّلَٰثَةِ ٱلَّذِينَ خُلِّفُواْ حَتَّىٰٓ إِذَا ضَاقَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلۡأَرۡضُ
بِمَا رَحُبَتۡ وَضَاقَتۡ عَلَيۡهِمۡ أَنفُسُهُمۡ وَظَنُّوٓاْ أَن لَّا مَلۡجَأَ
مِنَ ٱللَّهِ إِلَّآ إِلَيۡهِ ثُمَّ تَابَ عَلَيۡهِمۡ لِيَتُوبُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ
ٱلرَّحِيمُ ١١٨ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَكُونُواْ مَعَ
ٱلصَّٰدِقِينَ ١١٩ مَا كَانَ لِأَهۡلِ ٱلۡمَدِينَةِ وَمَنۡ حَوۡلَهُم
مِّنَ ٱلۡأَعۡرَابِ أَن يَتَخَلَّفُواْ عَن رَّسُولِ ٱللَّهِ وَلَا يَرۡغَبُواْ
بِأَنفُسِهِمۡ عَن نَّفۡسِهِۦۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ لَا يُصِيبُهُمۡ ظَمَأٞ
وَلَا نَصَبٞ وَلَا مَخۡمَصَةٞ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَلَا يَطَـُٔونَ مَوۡطِئٗا
يَغِيظُ ٱلۡكُفَّارَ وَلَا يَنَالُونَ مِنۡ عَدُوّٖ نَّيۡلًا إِلَّا كُتِبَ
لَهُم بِهِۦ عَمَلٞ صَٰلِحٌۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُضِيعُ أَجۡرَ ٱلۡمُحۡسِنِينَ
١٢٠ وَلَا يُنفِقُونَ نَفَقَةٗ صَغِيرَةٗ وَلَا كَبِيرَةٗ وَلَا يَقۡطَعُونَ
وَادِيًا إِلَّا كُتِبَ لَهُمۡ لِيَجۡزِيَهُمُ ٱللَّهُ أَحۡسَنَ مَا كَانُواْ
يَعۡمَلُونَ ١٢١ ۞ وَمَا كَانَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لِيَنفِرُواْ كَآفَّةٗۚ (نصف الحزب ٢١)
فَلَوۡلَا نَفَرَ مِن كُلِّ فِرۡقَةٖ مِّنۡهُمۡ طَآئِفَةٞ لِّيَتَفَقَّهُواْ فِي ٱلدِّينِ
وَلِيُنذِرُواْ قَوۡمَهُمۡ إِذَا رَجَعُوٓاْ إِلَيۡهِمۡ لَعَلَّهُمۡ يَحۡذَرُونَ ١٢٢



**(118) Kuma lallai Allah ya karvi tuban mutane ukun nan, wato, Ka'abu xan Malik, da Muraratu xan Rabe'u da Hilal xan Umayyah, waxanda aka jinkirtar da karvar tubansu, bayan basu fita tare da Manzon Allah (S.A.W) zuwa Yaqin Tabuka ba, sai Annabi ya yi umarni da cewa a qaurace musu, suka shiga cikin baqin ciki da alhini sakamakon haka, har duniya duk da faxinta ta yi masu qunci, zukatansu sun shiga cikin qunci sakamakon zaman qaxaici, suka tabbatar cewa basu da wata mafaka da za su fake da ita sai ga Allah, sai Allah ya jiqan su, Ya datar da su zuwa tuba, sannan Ya karvi tubansu. Haqiqa Allah mai yawan karvan tuban bayinsa ne, mai jinqai ne a gare su.**

**(119) Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, suka bi manzonsa, suka yi aiki da shari'arsa ku ji tsoron Allah ta hanyar bin umarninsa da nisantar haninsa, kuma ku zama cikin masu gaskiya cikin imaninsu da zantukansu da ayyukansu, domin baku da tafarkin tsira sai dai cikin gaskiya.**

**(120) Bai dace ba ga mutanen Madinah da mutanen da ke kewayensu ba, wato mazauna qauye, su zauna a baya, su qyale Manzon Allah (S.A.W) yayin da ya fita zuwa jihadi. Haka nan bai dace a gare su ba su so kansu, su bai wa kansu kariya su qyale Annabi (S.A.W). Dole ne a kansu su bayar da kawunansu don kare shi, saboda babu wani abin da zai same su, na qishirruwa ko gajiya ko yunwa akan tafarkin Allah, haka nan ba za su yada zango a wani mazauni ba da zai baqantawa kafirai rai ba, ko su afkawa wani kafiri da kisa, ko kamu, ko kwasar ganima, ko rushewa, face sai Allah ya rubuta musu ladan aikin nagari da ya karva daga wurinsu a sanadiyyar hakan. Haqiqa Allah ba ya tauye ladan masu kyautata aiki, sai dai yana cika musu ne kuma ya yi musu qari.**

**(121) Kuma ba za su tava bayar da wata dukiya ba, kaxan ko mai yawa, ba zasu tava qetare wani kwari ba, face sai an rubuta musu abin da suka yi na bayarwa da tafiya, saboda Allah ya saka musu a lahira, kuma ya basu ladan mafi kyawun abin da suka kasance suna aikatawa.**

**(122) Bai dace ga muminai su fita yaqi gaba xayansu ba, saboda kar a tumvuke su gaba xaya, yayin da abokan gabansu suka yi galaba a kansu. Ina ma da wasu vangare za su fita jihadi a cikinsu, wasu vangare kuma su tsaya, su zauna da Manzon Allah (S.A.W), su koyi ilimin addini daga abin da za su ji daga Annabi (S.A.W) na Alqur'ani da dokokin Shari'ah, kuma su yi wa mutanensu idan su dawo zuwa gare su wa'azi da abin da suka koya, da fatan ko za su kiyayi azabar Allah da uqubarsa, su kamanta umarninsa, su nisaci haninsa. Wannan hukunci ya shafi rundunonin yaqin da Manzon Allah (S.A.W) yake turawa ne zuwa sassa daban daban, ya zavi wasu vangare daga cikin sahabbansa su tafi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Wajabcin tsoron Allah da yin gaskiya domin su ne sababin tsira daga halaka.**

**2 - Girman falalar ciyarwa saboda Allah.**

**3 - Wajabcin neman ilimin addini, kamar yadda yake wajibi ne ayi jihadi, domin addini bai tsaya ba, sai da waxannan abubuwa guda biyu.**

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ قَٰتِلُوا۟ ٱلَّذِينَ يَلُونَكُم مِّنَ ٱلْكُفَّارِ
وَلْيَجِدُوا۟ فِيكُمْ غِلْظَةً ۚ وَٱعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلْمُتَّقِينَ
١٢٣ وَإِذَا مَآ أُنزِلَتْ سُورَةٌ فَمِنْهُم مَّن يَقُولُ أَيُّكُمْ زَادَتْهُ
هَٰذِهِۦٓ إِيمَٰنًا ۚ فَأَمَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ فَزَادَتْهُمْ إِيمَٰنًا وَهُمْ
يَسْتَبْشِرُونَ ١٢٤ وَأَمَّا ٱلَّذِينَ فِى قُلُوبِهِم مَّرَضٌ فَزَادَتْهُمْ
رِجْسًا إِلَىٰ رِجْسِهِمْ وَمَاتُوا۟ وَهُمْ كَٰفِرُونَ ١٢٥ أَوَلَا
يَرَوْنَ أَنَّهُمْ يُفْتَنُونَ فِى كُلِّ عَامٍ مَّرَّةً أَوْ مَرَّتَيْنِ
ثُمَّ لَا يَتُوبُونَ وَلَا هُمْ يَذَّكَّرُونَ ١٢٦ وَإِذَا مَآ
أُنزِلَتْ سُورَةٌ نَّظَرَ بَعْضُهُمْ إِلَىٰ بَعْضٍ هَلْ يَرَىٰكُم
مِّنْ أَحَدٍ ثُمَّ ٱنصَرَفُوا۟ ۚ صَرَفَ ٱللَّهُ قُلُوبَهُم بِأَنَّهُمْ قَوْمٌ
لَّا يَفْقَهُونَ ١٢٧ لَقَدْ جَآءَكُمْ رَسُولٌ مِّنْ أَنفُسِكُمْ
عَزِيزٌ عَلَيْهِ مَا عَنِتُّمْ حَرِيصٌ عَلَيْكُم بِٱلْمُؤْمِنِينَ
رَءُوفٌ رَّحِيمٌ ١٢٨ فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَقُلْ حَسْبِىَ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ
إِلَّا هُوَ ۖ عَلَيْهِ تَوَكَّلْتُ ۖ وَهُوَ رَبُّ ٱلْعَرْشِ ٱلْعَظِيمِ ١٢٩

آياتها ١٠٩ — سُورَةُ يُونُسَ — ترتيبها ١٠



**(123) Allah Maxaukakin Sarki ya umarci muminai da su yaqi waxanda suke maqwabtaka da su cikin kafirai, saboda haxarinsu ga muminai a dalilin kusancinsu. Haka nan ya umarci muminai su da su bayyana qarfi da tsananinsu don tsoratar da kafirai da munafukai da kawar da sharrinsu. Allah Maxaukakin Sarki yana tare da muminai masu taqawa da taimakonsa da qarfafawarsa.**

**(124) Idan Allah Ya saukar da wata sura ga Manzonsa (S.A.W) sai wasu cikin munafikai su riqa tambayar izgili cewa: "Waye a cikin ku wanda wannan surar da ta sauka ta qara masa imani da abin da Muhammadu ya zo da shi?" Amma waxanda suka yi imani da Allah, suka gasgata Manzonsa, to lallai su kam saukar da surar yana qara musu imani akan imaninsu da ya gabata, kuma suna farin ciki da abin da ya sauka na wahayi, saboda abin da yake ciki na amfaninsu na duniya da lahira.**

**(125) Amma munafukai kuwa to saukowar Alqur'ani, da abin da yake cikinsa na hukunce-hukunce da qissoshi, yana qara musu cuta ne da muni, saboda qaryatawarsu da abin da yake sauko wa cikinsa, sai cutar zuciyarsu ta qaru da qaruwar saukar Alqur'ani, domin duk lokacin da wani abu ya sauka sai sun yi shakku a cikinsa, kuma su mutu a kan kafirci.**

**(126) Shin munafikai baza su yi tunani su xauki izina daga jarrabawar da Allah yake yi musu, na bayyana halinsu da tona asirin munafincinsu a kowace shekara ba, sau xaya ko sau biyu ba? Duk da cewa suna da sanayyar cewa Allah shine yake yi musu hakan, amma baza su tuba daga kafircinsu ba, baza su daina munafincinsu ba, ba zasu tuna da abubuwan da suka faru da su ba, da cewa duka daga wurin Allah ba ne!**

**(127) Idan Allah ya saukar wa da Manzonsa (S.A.W) wata sura, wacce ta qunshi halayen munafikai, sai wasu dagan cikinsu su kalli sashe, suna cewa: "Akwai wanda yake ganinku ne?" Idan babu wanda yake ganinsu, sai su fice daga majalisin. Ku saurara! Allah ne Ya kawar da zukatansu daga shiriya da alheri, Ya tavar da su saboda kasancewarsu mutane ne marasa fahimta.**

**(128) Haqiqa Manzo ya zo muku – Ya ku taron Larabawa - daga jinsinku, wato balarabe ne shi irinku, duk abin da zai baku wahala yana masa nauyi, kuma yana tsananin qwaxayin shiriyarku da kulawa da ku, kuma dangane da muminai, shi mai yawan rangwame ne da jin qai.**

**(129) Idan sun juya maka baya, suka qi yin imani da abin da ka zo da shi, to ka ce musu – Ya kai wannan Manzo-Allah wanda babu abin bautawa da gaskiya sai shi, ya ishe mu, gare shi kaxai na dogara, kuma Shi ne mahallicin al'arshi mai girma.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Wajabcin fara yaqi da kafiran da suka fi kusa, idan qasar musulunci ta yi faxi kuma buqatar hakan ta taso.**

**2 - Bayanin halin munafikai yayin da Alqur'ani yake sauka a kansu wanda shi ne, dako da kai-kawo.**

**3 - Bayanin jin qan Annabi (S.A.W) ga muminai da kulawarsa gare su.**

**4 - A cikin ayoyin akwai dalili akan cewa imani yana qaruwa kuma yana raguwa. Kuma ya dace ga mumini ya riqa kula da imaninsa, yana kiyaye shi, yana sabunta shi, yana renonsa, domin ya kasance cikin qaruwa a kowane lokaci.**

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓر تِلْكَ ءَايَٰتُ ٱلْكِتَٰبِ ٱلْحَكِيمِ ١ أَكَانَ لِلنَّاسِ عَجَبًا
أَنْ أَوْحَيْنَآ إِلَىٰ رَجُلٍ مِّنْهُمْ أَنْ أَنذِرِ ٱلنَّاسَ وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوٓا۟ أَنَّ لَهُمْ قَدَمَ صِدْقٍ عِندَ رَبِّهِمْ ۗ قَالَ ٱلْكَٰفِرُونَ
إِنَّ هَٰذَا لَسَٰحِرٌ مُّبِينٌ ٢ إِنَّ رَبَّكُمُ ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضَ فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ ۖ يُدَبِّرُ ٱلْأَمْرَ ۖ
مَا مِن شَفِيعٍ إِلَّا مِنۢ بَعْدِ إِذْنِهِۦ ۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ فَٱعْبُدُوهُ ۚ
أَفَلَا تَذَكَّرُونَ ٣ إِلَيْهِ مَرْجِعُكُمْ جَمِيعًا ۖ وَعْدَ ٱللَّهِ حَقًّا ۚ إِنَّهُۥ
يَبْدَؤُا۟ ٱلْخَلْقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ لِيَجْزِىَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟
ٱلصَّٰلِحَٰتِ بِٱلْقِسْطِ ۚ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لَهُمْ شَرَابٌ مِّنْ حَمِيمٍ
وَعَذَابٌ أَلِيمٌۢ بِمَا كَانُوا۟ يَكْفُرُونَ ٤ هُوَ ٱلَّذِى جَعَلَ ٱلشَّمْسَ
ضِيَآءً وَٱلْقَمَرَ نُورًا وَقَدَّرَهُۥ مَنَازِلَ لِتَعْلَمُوا۟ عَدَدَ ٱلسِّنِينَ
وَٱلْحِسَابَ ۚ مَا خَلَقَ ٱللَّهُ ذَٰلِكَ إِلَّا بِٱلْحَقِّ ۚ يُفَصِّلُ ٱلْءَايَٰتِ
لِقَوْمٍ يَعْلَمُونَ ٥ إِنَّ فِى ٱخْتِلَٰفِ ٱلَّيْلِ وَٱلنَّهَارِ وَمَا خَلَقَ
ٱللَّهُ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يَتَّقُونَ ٦



# Suratu Yunus

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Fuskantar masu qaryata wahayi da hujjoji da dalilai, tare da kiransu zuwa ga yin imani ta hanyar kwaxaitarwa da tsoratarwa.**

## Tafsir:

**(1) Alif Lam Raa. Bayani ya gabata dangane da waxannan haruffa a farkon Suratul Baqara. Waxannan ayoyin da ake karantawa a cikin wannan surar, ayoyi ne na Alqur'ani, wanda aka kyautata shi, mai qunshe da hikima da hukunce-hukunce.**

**(2) Shin abin mamaki ne ga mutane don mun saukar da wahayi ga wani mutum irinsu, muna umartarsa da ya ya yi musu gargaxi daga azabar Allah?!. Ka yi wa muminai bushara – Ya kai wannan Manzo - da cewa suna da matsayi mai girma, saboda abin da suka gabatar na aikin qwarai a wajen Ubangijinsu Maxaukakin Sarki. Kafirai suka ce: "Wannan mutumin da ya zo da waxannan ayoyin lallai mai sihiri ne bayyananne".**

**(3) Haqiqa Ubangijinku – Ya ku masu yin mamaki- shi ne fa Allah wanda ya halicci sammai duk da girmansu, da qasa duk da faxinta a cikin kwanaki shida, sannan ya xaukaka a kan Al'arshi. To ta yaya zaku yi mamaki don ya aiko muku da Manzo daga jinsinku?! Alhali shi kaxai ne yake yanke hukunci, yake da iko a cikin mulkinsa mai yalwa, babu wanda yake da ikon yin ceto a wajensa, sai da izininsa da yardarsa ga wanda za a cece ta xin. Wanda ya siffantu da waxannan siffofin shi ne Allah Ubangijinku, don haka ku kaxaita shi da bauta shi qaxai. Shin ba zaku wa'azantu ba da dukkanin waxannan hujjoji da dalilai akan kaxaituwarsa? Duk wanda yake jin wa'azi komai qanqantarsa ya san haka, kuma ya bayar da gaskiya da shi. (4) Zuwa ga Allah shi kaxai zaku koma a ranar alqiyama, don ya saka muku akan ayyukanku. Wannan alqawari ne da Allah ya yi wa mutane, alqawari na gaskiya da ba zai sava shi ba. Haqiqa shi mai iko ne akan haka. Shi yake fara samar da abin halitta ba tare da ya ga samfur a wurin wani ba, sannan ya dawo da ita bayan mutuwarta, don ya sakawa waxanda suka yi imani da Allah kuma suka yi ayyuka nagari da adalci, ba tare da ya rage musu komai na ladan kyawawan ayyukansu ba, kuma ba tare da ya qara musu yawan munanan ayyukansu ba. Amma waxanda suka kafirce wa Allah da Manzanninsa kuwa to suna da azabar abin sha, tafasasshen ruwa wanda ya kai matuqa wajen tafasa, zai tsintsinke hanjinsu, kuma suna da azaba mai raxaxi saboda kafircinsu da Allah da Manzanninsa. (5) Shi ne Ya sanya rana take bayar da haske, kuma ta raba shi ko'ina da ina, kuma ya sanya wata ya zama haske da ake haskakawa da shi, ya qaddara masa wurin da yake tafiya a ciki, matakai daban daban har guda ishirin da takwas. gwargwadon kowace tafiya tsakanin wani mataki da wani tsawon yini da dare xaya ne, Allah ya yi haka ne don – ku mutane- ku san lissafin kwanaki ta hanyar rana, da lissafin watanni da shekaru ta hanyar wata, Allah bai halicci sammai da qassai da abin da ke cikinsu ba face sai da gaskiya, domin ya bayyana ikonsa da girmansa ga mutane. Allah yana bayyana waxannan dalilai na fili da hujjoji bayyanannu akan kaxaitakarsa, ga mutanen da suka san kafa hujja da su a kan haka.**

**(6) Lallai a cikin bibiyar juna tsakanin dare da yini, da abin da yake cikinsu na haske da duhu, da gajartar wani da tsawon wani, da halittun da suke cikin sammai da qassai, akwai alamomin da suke nuna ikon Allah ga mutanen da suke tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa da nisantar abubuwan da ya hana.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tabbatar da Annabtar Annabi Muhammad (S.A.W) da bayanin cewa aiko shi abu ne na hankali, babu abin mamaki a ciki. 2 - Halittar sammai da qassai da abin da ke cikinsu, da tsara al'amura, da qaddara lokuta, da sassavawar dare da yini, dukkaninsu ayoyi ne masu girma, da suke nuna allantakar Allah Maxaukakin Sarki. 3 - Ceto a ranar alqiyama ba zai kasance ba sai ga wanda Allah ya ba shi izini, kuma ya yarda da maganarsa da aikinsa. 4 - Tsara tafiyar rana da tafiyar wata, yana taimaka wa wajen kiyaye tarihi da sanin lissafin kwanaki da shekaru.**

إِنَّ ٱلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ لِقَآءَنَا وَرَضُواْ بِٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَٱطۡمَأَنُّواْ
بِهَا وَٱلَّذِينَ هُمۡ عَنۡ ءَايَٰتِنَا غَٰفِلُونَ ٧ أُوْلَٰٓئِكَ مَأۡوَىٰهُمُ
ٱلنَّارُ بِمَا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ٨ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ
ٱلصَّٰلِحَٰتِ يَهۡدِيهِمۡ رَبُّهُم بِإِيمَٰنِهِمۡۖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهِمُ
ٱلۡأَنۡهَٰرُ فِي جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ٩ دَعۡوَىٰهُمۡ فِيهَا سُبۡحَٰنَكَ
ٱللَّهُمَّ وَتَحِيَّتُهُمۡ فِيهَا سَلَٰمٞۚ وَءَاخِرُ دَعۡوَىٰهُمۡ أَنِ ٱلۡحَمۡدُ
ثلاثة أرباع الحزب ٢١ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٠ ۞وَلَوۡ يُعَجِّلُ ٱللَّهُ لِلنَّاسِ ٱلشَّرَّ
ٱسۡتِعۡجَالَهُم بِٱلۡخَيۡرِ لَقُضِيَ إِلَيۡهِمۡ أَجَلُهُمۡۖ فَنَذَرُ ٱلَّذِينَ
لَا يَرۡجُونَ لِقَآءَنَا فِي طُغۡيَٰنِهِمۡ يَعۡمَهُونَ ١١ وَإِذَا مَسَّ ٱلۡإِنسَٰنَ
ٱلضُّرُّ دَعَانَا لِجَنۢبِهِۦٓ أَوۡ قَاعِدًا أَوۡ قَآئِمٗا فَلَمَّا كَشَفۡنَا
عَنۡهُ ضُرَّهُۥ مَرَّ كَأَن لَّمۡ يَدۡعُنَآ إِلَىٰ ضُرّٖ مَّسَّهُۥۚ كَذَٰلِكَ زُيِّنَ
لِلۡمُسۡرِفِينَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٢ وَلَقَدۡ أَهۡلَكۡنَا ٱلۡقُرُونَ
مِن قَبۡلِكُمۡ لَمَّا ظَلَمُواْ وَجَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ وَمَا كَانُواْ
لِيُؤۡمِنُواْۚ كَذَٰلِكَ نَجۡزِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ١٣ ثُمَّ جَعَلۡنَٰكُمۡ
خَلَٰٓئِفَ فِي ٱلۡأَرۡضِ مِنۢ بَعۡدِهِمۡ لِنَنظُرَ كَيۡفَ تَعۡمَلُونَ ١٤



**(7) Haqiqa kafirai waxanda basa tunanin haxuwa da Allah, ballantana su ji tsoronsa, ko su yi kwaxayin rahamarsa. Kuma sun yarda da rayuwar duniya mai qarewa a madadin rayuwar lahira mai xorewa, kuma zukatansu sun nutsu da ita, suna farin ciki da ita, da kuma waxanda su dangane da ayoyin Allah da dalilansa masu kawar da kai ne da shagala.**

**(8) Masu waxannan siffofi makomarsu da za su tabbata a cikinta, ita ce wuta, saboda abin da suka aikata na kafirci da qaryatawa da ranar alqiyama.**

**(9) Lallai wanxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi kyawawan ayyuka, to Allah zai azurta su da shiriya zuwa aiki nagari, mai kai wa zuwa ga yardarsa, saboda imaninsu, sannan ranar alqiyama zai shigar da su Aljannatai na ni'ima, waxanda qoramu ke gudana a qarqashin su.**

**(10) Addu'arsu a cikin Aljanna ita ce: Tsarkake Allah da girmama shi, kuma gaisuwar Allah a gare su da gaisuwar Mala'iku da gaisuwarsu ga junansu ita ce Aminci ya tabbata a gare ku. Kuma qarshen addu'arsu yabo ne ga Allah Mahallicin halitta baki xaya.**

**(11) Da a ce Allah Maxaukakin Sarki yana gaggauta amsa addu'ar da mutane suke yi wa kawunansu da 'ya'yansu da dukiyoyinsu ta sharri a yayin da suka yi fushi, irin yadda yake amsa addu'arsu ta alheri, da sun halaka, sai dai Allah yana jinkirta musu, sai ya qyale waxanda basa jiran haxuwa da shi – domin basa tsoron wata uquba ko fatan wani lada - sai ya qyale su suna ta fagamniya cikin ruxu da shakku dangane da ranar hisabi.**

**(12) Idan cuta ko mummunan yanayi suka shafi mutumin da yake wa kansa shishshigi, sai ya kira mu, yana mai qasqantar da kansa, a kwance yake akan haqarqarinsa, ko a zaune, ko kuma a tsaye, yana mai fatan a kawar masa da abin da ya same shi na cuta, amma da zarar mun amsa addu'arsa, mun kawar masa da cutar da ta shafe shi, sai ya koma kan yanayinsa da ya kasance a ciki, kamar bai tava kiran mu don mu yaye masa wata cuta da ta same shi ba. To kamar yadda aka qawata wa wannan mai kawar da kai xin, ya yi nisa a cikin vatansa, haka nan ne aka qawata wa masu qetare iyakoki abin da suka kasance suna aikatawa na kafirci da savo, don haka ba sa iya barinsu.**

**(13) Kuma lallai mun halaka waxansu al'ummomi gabaninku – Ya ku Mushirikai - saboda qaryata Manzannin Allah da suka yi, da aikata savo. Kuma tabbas Manzanninsu waxanda muka aiko musu sun zo musu da hujjoji bayyanannu, masu nuni akan gaskiyarsu cikin abin da suka zo da shi daga wurin Ubangijinsu, amma ba su yi imani ba, saboda rashin shirinsu na karvar gaskiya, sai Allah ya tavar da su, bai yi musu dace ba, kamar yadda muka sakawa waxancan al'ummomi masu zalunci, haka zamu sakawa ire-irensu a kowane lokaci, da kowane wuri.**

**(14) Sannan sai muka sanyaku – Ya ku mutane- kuka zama waxanda suka maye gurbin waxancan al'ummomi, masu qaryata Manzanni, wanxanda muka halaka su, domin muga yadda zaku yi, shin zaku yi alheri ne sai a baku lada a kai, ko zaku yi sharri ne sai a yi muku uquba a kansa?.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tausayin Allah ga bayinsa cikin rashin amsa addu'o'insu na sharri da suke yi wa kawunansu da 'ya'yansu.**

**2 - Bayanin halin mutum wajen yin addu'a cikin qunci, da kawar da kai a lokacin yalwa, da yin gargaxi akan siffantuwa da hakan.**

**3 - Halakar da al'ummomi da suka gabata ya kasance ne a sakamakon aikata savo da zaluncin da suka yi.**

وَإِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِمۡ ءَايَاتُنَا بَيِّنَٰتٖ قَالَ ٱلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ
لِقَآءَنَا ٱئۡتِ بِقُرۡءَانٍ غَيۡرِ هَٰذَآ أَوۡ بَدِّلۡهُۚ قُلۡ مَا يَكُونُ
لِيٓ أَنۡ أُبَدِّلَهُۥ مِن تِلۡقَآيِٕ نَفۡسِيٓۖ إِنۡ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَيَّۖ
إِنِّيٓ أَخَافُ إِنۡ عَصَيۡتُ رَبِّي عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ ١٥ قُل
لَّوۡ شَآءَ ٱللَّهُ مَا تَلَوۡتُهُۥ عَلَيۡكُمۡ وَلَآ أَدۡرَىٰكُم بِهِۦۖ
فَقَدۡ لَبِثۡتُ فِيكُمۡ عُمُرٗا مِّن قَبۡلِهِۦٓۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ١٦
فَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّنِ ٱفۡتَرَىٰ عَلَى ٱللَّهِ كَذِبًا أَوۡ كَذَّبَ بِـَٔايَٰتِهِۦٓۚ
إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ ١٧ وَيَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
مَا لَا يَضُرُّهُمۡ وَلَا يَنفَعُهُمۡ وَيَقُولُونَ هَٰٓؤُلَآءِ شُفَعَٰٓؤُنَا
عِندَ ٱللَّهِۚ قُلۡ أَتُنَبِّـُٔونَ ٱللَّهَ بِمَا لَا يَعۡلَمُ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا
فِي ٱلۡأَرۡضِۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ١٨ وَمَا
كَانَ ٱلنَّاسُ إِلَّآ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ فَٱخۡتَلَفُواْۚ وَلَوۡلَا كَلِمَةٞ
سَبَقَتۡ مِن رَّبِّكَ لَقُضِيَ بَيۡنَهُمۡ فِيمَا فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ
١٩ وَيَقُولُونَ لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡهِ ءَايَةٞ مِّن رَّبِّهِۦۖ فَقُلۡ إِنَّمَا
ٱلۡغَيۡبُ لِلَّهِ فَٱنتَظِرُوٓاْ إِنِّي مَعَكُم مِّنَ ٱلۡمُنتَظِرِينَ ٢٠



**15 Idan aka karanta ayoyin Alqur'ani bayyanannu masu nuni akan kaxaita Allah da bauta, sai masu inkarin tashin alqiyama, waxanda basa fatan lada, kuma basa tsoron uquba, su ce: "Kawo mana wani Alqur'anin ba wannan AlQur'anin da yake qunshe da zagin bautar gumaka ba, ko kuma ka canza shi, ta hanyar soke wani sashensa ko gaba xayansa da abin da zai dace da abin da zukatanmu suke so". To kace musu –Ya kai wannan Manzo-: " Ba zai yiwu ni in musanya shi ba, ballantana ma in iya zuwa da waninsa!, Allah ne kaxai yake da ikon canza abin da ya ga dama a cikinsa, ni ba abin da nake bi, face abin da aka yi wahayin sa zuwa gare ni. Lallai ni ina jin tsoro, in har na savawa Allah ta hanyar amsawa abin da kuke nema, to ina jin tsoron azabar wata rana mai girma. Ita ce ranar alqiyama".**

**16 Ya kai wannan Manzo ka ce -: "Da Allah ya ga damar kar in karanta muku Alqur'ani da ban karanta muku ba, kuma da ban isar muku da shi ba. Haka da Allah ya ga dama da bai sanar da ku Alqur'ani akan harshe na ba, ai na zauna a cikinku lokaci mai tsawo, wato shekara arba'in, bana karatu, bana rubutu, bana neman wannan lamari, bana bincikensa. Ashe ba zaku yi amfani da hankalinku ku riski cewa wannan abin da na zo da shi daga Allah yake ba, ba ni da wani sha'ani a cikinsa?".**

**17 Babu wanda ya fi zalunci fiye da wanda ya qirqiri qarya ya jingina wa Allah. Ta yaya zai yiwu in musanya Alqur'ani ta hanyar qirqirar qarya. Gaskiyar lamarin shi ne, masu qetare iyakokin Allah ta hanyar yi masa qire ba sa rabauta da samun biyan buqatunsu.**

**18 Mushirikai suna bautawa wasu abubuwan bauta da suke riyawa koma bayan Allah, waxanda basa amfanarwa, basa cutarwa, alhali abin bauta da gaskiya kuwa yana amfanarwa, yana cutarwa a duk lokacin da ya ga dama. Suna cewa dangane da abubuwan bautarsu: "Waxannan tsani ne, zasu cece mu a wurin Allah, don haka ba zai yi mana azabar zunubanmu ba". To ka ce musu – Ya kai wannan Manzo-: "Shin kuna ba wa Allah labarin cewa yana da abokin tarayya ne?, alhali shi bai san yana da wani abokin tarayya a cikin sammai ko qassai ba! Allah ya tsarkaka, daga abin da mushirikai suke faxa na varna da qarya.**

**19 Mutane basu kasance ba face al'umma guda xaya, mai imani, mai kaxaita Allah da bauta, amma daga baya sai suka yi savani. A cikinsu akwai waxanda suka tabbata a kan imaninsu, akwai kuma waxanda suka kafirce. Ba don abin da ya riga ya gudana na hukuncin Allah ba, cewa ba zai yanke musu hukunci a cikin abubuwan da suka yi savani cikinsu a nan duniya ba, zai musu hukunci ne a cikinsu ranar alqiyama, ba don haka ba, da ya yanke hukunci a tsakaninsu a nan duniya, cikin abin da suke savani a ciki, don a gane wane ne shiryayye kuma wane ne vatacce.**

**20 Mushirikai suna cewa: "A saukar wa Muhammad alama mana daga Ubangijinsa wacce zata tabbatar da gaskiyarsa?". To kace musu –Ya kai wannan Manzo -: "Saukar alamomi (wato ayoyi) gaibu ne daga Allah, da ya keve kansa da saninsa. Don haka ku jira abubuwan da kuka nema na alamomi na zahiri, ni ma ina nan tare da ku ina jiran su".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Girman munin qire da qarya ga Allah da canza zancensa, kamar yadda Yahudawa suka yi wa Attaura.**
**2 - Amfanarwa da cutarwa a hannun Allah Maxaukakin Sarki suke, shi kaxai bai da abokin tarayya.**
**3 - Vacin zancen Mushirikai na cewa abubuwan bautansu za su cece su a wurin Allah.**
**4 - Bin son rai da savani kan addini su ne ke janyo rabuwar kai.**

وَإِذَآ أَذَقۡنَا ٱلنَّاسَ رَحۡمَةٗ مِّنۢ بَعۡدِ ضَرَّآءَ مَسَّتۡهُمۡ إِذَا لَهُم مَّكۡرٞ
فِيٓ ءَايَاتِنَاۚ قُلِ ٱللَّهُ أَسۡرَعُ مَكۡرًاۚ إِنَّ رُسُلَنَا يَكۡتُبُونَ مَا تَمۡكُرُونَ
٢١ هُوَ ٱلَّذِي يُسَيِّرُكُمۡ فِي ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِۖ حَتَّىٰٓ إِذَا كُنتُمۡ فِي ٱلۡفُلۡكِ
وَجَرَيۡنَ بِهِم بِرِيحٖ طَيِّبَةٖ وَفَرِحُواْ بِهَا جَآءَتۡهَا رِيحٌ عَاصِفٞ
وَجَآءَهُمُ ٱلۡمَوۡجُ مِن كُلِّ مَكَانٖ وَظَنُّوٓاْ أَنَّهُمۡ أُحِيطَ بِهِمۡ
دَعَوُاْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ لَئِنۡ أَنجَيۡتَنَا مِنۡ هَٰذِهِۦ لَنَكُونَنَّ
مِنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ٢٢ فَلَمَّآ أَنجَىٰهُمۡ إِذَا هُمۡ يَبۡغُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ
ٱلۡحَقِّۗ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّمَا بَغۡيُكُمۡ عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمۖ مَّتَٰعَ ٱلۡحَيَوٰةِ
ٱلدُّنۡيَاۖ ثُمَّ إِلَيۡنَا مَرۡجِعُكُمۡ فَنُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٢٣
إِنَّمَا مَثَلُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا كَمَآءٍ أَنزَلۡنَٰهُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَٱخۡتَلَطَ
بِهِۦ نَبَاتُ ٱلۡأَرۡضِ مِمَّا يَأۡكُلُ ٱلنَّاسُ وَٱلۡأَنۡعَٰمُ حَتَّىٰٓ إِذَآ
أَخَذَتِ ٱلۡأَرۡضُ زُخۡرُفَهَا وَٱزَّيَّنَتۡ وَظَنَّ أَهۡلُهَآ أَنَّهُمۡ قَٰدِرُونَ
عَلَيۡهَآ أَتَىٰهَآ أَمۡرُنَا لَيۡلًا أَوۡ نَهَارٗا فَجَعَلۡنَٰهَا حَصِيدٗا كَأَن لَّمۡ تَغۡنَ
بِٱلۡأَمۡسِۚ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَتَفَكَّرُونَ ٢٤ وَٱللَّهُ يَدۡعُوٓاْ
إِلَىٰ دَارِ ٱلسَّلَٰمِ وَيَهۡدِي مَن يَشَآءُ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ٢٥



**21** **Idan muka xanxanawa mushirikai wata ni'ima, ta ruwan sama, ko kyan yanayi bayan fari da tsanani da ya same su, sai ka ga suna yin izgili, suna qaryata ayoyinmu. To ka ce wa waxannan Mushirikan -Ya kai wannan Manzo -: "Allah ya fi ku gaggawa wajen warware makircinku, kuma ya fi ku gaggawar yi muku talala da uquba, kuma tabbas Mala'iku suna rubuta duk abin da kuke tsarawa na makirci, babu abin da yake kubce musu. To yaya zai kubce wa Mahallicinsu?! Da sannu zai saka muku akan makircinku".**

**22** **Allah shi ne yake tafiyar da ku – Ya ku mutane-a kan tudu, akan qafafuwanku, ko dabbobinku, kuma shi ne ke tafiyar da ku akan tekuna cikin jiragen ruwa, har idan kuna cikin jiragen ruwa akan teku, iska mai daxi ta kaxa, sai waxanda suke cikin jirgin su yi farin ciki da iskar mai daxi, suna cikin wannan farin cikin, sai iska mai qarfi ta taso, kumfar teku ta yi wo kansu ta ko'ina, har sai sun tabbatar halaka za su yi, sai su kira Allah shi kaxai, baza su haxa shi da kowa ba, su ce, "Ya Allah idan ka tseratar damu daga wannan jarrabawar mai halakarwa, to zamu kasance cikin masu godewa ni'imar da ka yi mana".**

**23** **Amma yayin da ya amsa addu'arsu, ya kuvutar dasu daga wannan masifar, sai ka ga suna varna a bayan qasa, ta hanyar aikata kafirci da savo da zunubai. To ku farka – Ya ku mutane - Qarshen mummunan zaluncinku zai koma ne a kanku, zaluncinku baya cutar da Allah, kuna da jin daxi da shi a rayuwarku ta duniya mai qarewa, sannar makomarku tana gare mu ranar alqiyama, mu baku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa na zunubi, kuma mu saka muku a kan hakan.**

**24** **Misalin rayuwar duniya wacce kuke jin daxi a cikinta, wajen saurin qarewarta, kamar ruwan sama ne, wanda ya haxu da tsiron qasa, na daga abin da mutane suke ci, na qwayoyi da kayan marmari, da wanda dabbobi ma suke ci, na ganye da sauransu, har zuwa lokacin da qasa zata yi kyau tana qyalqyali, ta yi ado da abin da take fitarwa na tsirrai kala-kala, masu wannan shuka sun yi zaton suna da ikon girbe abin da ta fitar na tsirrai, kwatsam sai hukuncinmu na halaka ya zo, sai muka mayar da shi girbabbe, kamar ba ita ba ce cike da bishiyoyi da tsirrai ba a baya. To Kamar yadda muka bayyana muku halin duniya da saurin qarewarta, haka muke bayyana muku dalilai da hujjoji, domin ku yi tunani ku dauki izna.**

**25** **Allah yana kiran mutane baki xayansu zuwa ga Aljannarsa wacce ita ce gidan aminci, mutane za su aminta a cikinta daga masifu da baqin ciki, kuma su quvuta daga mutuwa. Allah Shi yake yin dace ga wanda ya ga dama ciki bayinsa zuwa ga addinin Musulunci, wanda ke kai wa zuwa wannan gida na aminci.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Allah Shi yafi saurin damqar duk wanda yake yin makirci ga bayinsa muminai.**

**2 - Zaluncin mutum yana komawa ne a kansa, baya cutar da kowa sai kansa.**

**3 - Bayanin haqiqanin duniya wajen saurin qarewarta da gushewarta, hakanan abin da ke cikinta na ni'ima shi ma mai qarewa ne.**

**4 - Aljannah ita ce makomar mumini, saboda abin da ke cikinta na ni'ima da aminta daga masifu da dangin baqin ciki.**

الحزب ٢٢

۞ لِّلَّذِينَ أَحْسَنُوا۟ ٱلْحُسْنَىٰ وَزِيَادَةٌ ۖ وَلَا يَرْهَقُ وُجُوهَهُمْ قَتَرٌ
وَلَا ذِلَّةٌ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٢٦ وَٱلَّذِينَ
كَسَبُوا۟ ٱلسَّيِّـَٔاتِ جَزَآءُ سَيِّئَةٍۭ بِمِثْلِهَا وَتَرْهَقُهُمْ ذِلَّةٌ ۖ مَّا لَهُم
مِّنَ ٱللَّهِ مِنْ عَاصِمٍ ۖ كَأَنَّمَآ أُغْشِيَتْ وُجُوهُهُمْ قِطَعًا مِّنَ ٱلَّيْلِ
مُظْلِمًا ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٢٧ وَيَوْمَ نَحْشُرُهُمْ
جَمِيعًا ثُمَّ نَقُولُ لِلَّذِينَ أَشْرَكُوا۟ مَكَانَكُمْ أَنتُمْ وَشُرَكَآؤُكُمْ ۚ فَزَيَّلْنَا
بَيْنَهُمْ ۖ وَقَالَ شُرَكَآؤُهُم مَّا كُنتُمْ إِيَّانَا تَعْبُدُونَ ٢٨ فَكَفَىٰ بِٱللَّهِ
شَهِيدًۢا بَيْنَنَا وَبَيْنَكُمْ إِن كُنَّا عَنْ عِبَادَتِكُمْ لَغَٰفِلِينَ ٢٩
هُنَالِكَ تَبْلُوا۟ كُلُّ نَفْسٍ مَّآ أَسْلَفَتْ ۚ وَرُدُّوٓا۟ إِلَى ٱللَّهِ مَوْلَىٰهُمُ
ٱلْحَقِّ ۖ وَضَلَّ عَنْهُم مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ٣٠ قُلْ مَن يَرْزُقُكُم مِّنَ
ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ أَمَّن يَمْلِكُ ٱلسَّمْعَ وَٱلْأَبْصَٰرَ وَمَن يُخْرِجُ
ٱلْحَىَّ مِنَ ٱلْمَيِّتِ وَيُخْرِجُ ٱلْمَيِّتَ مِنَ ٱلْحَىِّ وَمَن يُدَبِّرُ ٱلْأَمْرَ ۚ
فَسَيَقُولُونَ ٱللَّهُ ۚ فَقُلْ أَفَلَا تَتَّقُونَ ٣١ فَذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمُ
ٱلْحَقُّ ۖ فَمَاذَا بَعْدَ ٱلْحَقِّ إِلَّا ٱلضَّلَٰلُ ۖ فَأَنَّىٰ تُصْرَفُونَ ٣٢ كَذَٰلِكَ
حَقَّتْ كَلِمَتُ رَبِّكَ عَلَى ٱلَّذِينَ فَسَقُوٓا۟ أَنَّهُمْ لَا يُؤْمِنُونَ ٣٣



**(26) Waxanda suka kyautata aiki ta hanyar tsayar da abubuwan da Allah ya wajabta musu na biyayya, da barin abubuwan da ya haramta musu na savo, suna da sakamako mafi kyau, shi ne Aljannah, da qarin wani abu a kan haka, shi ne kallon fuskar Allah Maxaukakin Sarki, sannan kuma qura ba za ta lulluve fuskokinsa, wulakanci da tavewa ba zasu shafe su ba. Waxannan masu kyautatawar su ne 'yan Aljannah, masu zama a cikinta ne din-din-din. (27) Wanxanda suka aikata munanan ayyuka na kafirci da savo suna da sakamakon mummunan aikin da suka yi gwargwadon abin da suka yi na uqubar Allah a lahira, Qasqanci da wulaqanci zasu lulluve su, basu da wani mai kariya da zai kare su daga azabar Allah idan ya saukar da ita a kansu, kai ka ce kamar an saka wa fuskokinsu baqin duhun dare saboda yawan abin da ya lulluvesu na hayaqin wuta da baqinta. Waxannan masu siffantuwa da waxannan siffofin su ne 'yan wuta, masu zaman din-din-din a cikinta har abada.**

**(28) Ka tuna – Ya kai wannan Manzo - ranar lahira yayin da zamu tara halittu gaba xaya, sannan mu ce da waxanda suka yi tarayya da Allah a wajen bauta masa: "Ya ku Mushrikai ku tsaya a matsayinku, ku da abubuwan bautarku, waxanda kuka kasance kuna bauta musu koma bayan Allah. Sai mu rarrabe tsakanin abubuwan bautar da masu bauta musu, Abubuwan bautar sai su barranta daga masu yi musu bauta, su ce musu: "Ba mu kuke bautawa ba a duniya".**

**(29) A nan ne allolinsu da suka bautawa koma bayan Allah za su barranta da su, su ce musu: "Allah ne shaida - kuma ya ishe mu shaida - cewa mu bamu yarda da bautar da kuke mana ba, kuma bamu yi muku umarni da yin ta ba, kuma bamu da masaniya dangane da bautarku. (30) A wannan matsayi mai girma ne kowace rai zata gwada abin da ta gabatar na aiki a rayuwarta ta duniya, za a mayar da Mushrikai zuwa wajen Ubangijinsu na gaskiya wanda shi ne Allah wanda shi ne zai yi musu hisabi, abin da suka qirqira na ceton gumakansu ya tafi daga gare su.**

**(31) Ya kai wannan Manzo, ka ce wa wanxannan masu tarayya da Allah cikin bauta: "Wa yake wadata ku daga sama ta hanyar saukar da ruwan sama a gareku? Kuma wa yake wadata ku daga qasa ta hanyar abin da yake tsira cikinta na tsiro, da abin da ta qunsa na ma'adinai? Kuma wa yake fitar da rayayye daga matacce, kamar mutum daga xigon maniyyi, da stuntsu daga qwai. Haka nan dai wa yake fitar da matacce daga cikin rayayye, kamar xigon maniyyi daga dabba, da qwai daga tsuntsu? Kuma wa yake gudanar da lamarin sammai da qassai da abin da ke cikinsu na halittu? Za su amsa maka cewa mai yin wannan duka shi ne Allah, to ka ce da su: "To baza ku san hakan ba, ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa da nesantar abubuwan da ya hana ba?**

**(32) Wannan fa - Ya ku mutane-, wanda yake aikata waxancan abubuwa duka shi ne Allah na gaskiya Mahaliccinku, Mai gudanar da lamarinku. To me ya rage bayan sanin gaskiya da qinta ban da nisantarta da lalacewa?! Ina hankulanku suke tafiya ne daga barin wannan gaskiyar bayyananniya?!.**

**(33) Kamar yadda Ubangijintaka ta gaskiya ta tabbata ga Allah, haka ma – Ya kai wannan Manzo - Zancen Ubangijinka na abin da ya qaddara ya tabbata akan waxanda suka qi bin gaskiya don taurin kai, na cewa ba za su tava yi imani ba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Mafi girman ni'imar da ake kwaxaitar da mumini ita, ita ce, ganin fuskar Allah Maxaukakin Sarki. 2 - Bayanin ikon Allah, da sanin cewa shi mai iko ne akan komai. 3 - Kaxaita Allah da a cikin ayyukansa, tare da haxa shi da wani cikin bauta varna ne. Dole ne a kaxaita Allah cikin duka abubuwan biyun, wato kaxaita Allah a ayyukansa da bauta masa.**

**4 - Idan Allah ya hukunta rashin imanin wasu mutane a sakamakon savonsu, to baza su tava yin imani ba.**

قُلۡ هَلۡ مِن شُرَكَآئِكُم مَّن يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥۚ قُلِ ٱللَّهُ يَبۡدَؤُاْ
ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥۖ فَأَنَّىٰ تُؤۡفَكُونَ ٣٤ قُلۡ هَلۡ مِن شُرَكَآئِكُم مَّن يَهۡدِيٓ
إِلَى ٱلۡحَقِّۚ قُلِ ٱللَّهُ يَهۡدِي لِلۡحَقِّۗ أَفَمَن يَهۡدِيٓ إِلَى ٱلۡحَقِّ أَحَقُّ أَن
يُتَّبَعَ أَمَّن لَّا يَهِدِّيٓ إِلَّآ أَن يُهۡدَىٰۖ فَمَا لَكُمۡ كَيۡفَ تَحۡكُمُونَ ٣٥
وَمَا يَتَّبِعُ أَكۡثَرُهُمۡ إِلَّا ظَنًّاۚ إِنَّ ٱلظَّنَّ لَا يُغۡنِي مِنَ ٱلۡحَقِّ شَيۡـًٔاۚ
إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمُۢ بِمَا يَفۡعَلُونَ ٣٦ وَمَا كَانَ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانُ أَن يُفۡتَرَىٰ
مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَٰكِن تَصۡدِيقَ ٱلَّذِي بَيۡنَ يَدَيۡهِ وَتَفۡصِيلَ ٱلۡكِتَٰبِ
لَا رَيۡبَ فِيهِ مِن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٣٧ أَمۡ يَقُولُونَ ٱفۡتَرَىٰهُۖ قُلۡ فَأۡتُواْ
بِسُورَةٖ مِّثۡلِهِۦ وَٱدۡعُواْ مَنِ ٱسۡتَطَعۡتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ
٣٨ بَلۡ كَذَّبُواْ بِمَا لَمۡ يُحِيطُواْ بِعِلۡمِهِۦ وَلَمَّا يَأۡتِهِمۡ تَأۡوِيلُهُۥۚ كَذَٰلِكَ
كَذَّبَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۖ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلظَّٰلِمِينَ ٣٩
وَمِنۡهُم مَّن يُؤۡمِنُ بِهِۦ وَمِنۡهُم مَّن لَّا يُؤۡمِنُ بِهِۦۚ وَرَبُّكَ أَعۡلَمُ
بِٱلۡمُفۡسِدِينَ ٤٠ وَإِن كَذَّبُوكَ فَقُل لِّي عَمَلِي وَلَكُمۡ عَمَلُكُمۡۖ أَنتُم
بَرِيٓـُٔونَ مِمَّآ أَعۡمَلُ وَأَنَا۠ بَرِيٓءٞ مِّمَّا تَعۡمَلُونَ ٤١ وَمِنۡهُم مَّن
يَسۡتَمِعُونَ إِلَيۡكَۚ أَفَأَنتَ تُسۡمِعُ ٱلصُّمَّ وَلَوۡ كَانُواْ لَا يَعۡقِلُونَ ٤٢



**(34) Ya kai wannan Manzo, ka cewa waxannan Mushirikai: "Shin akwai a cikin abubuwan tarayyarku da kuke bautawa koma bayan Allah, akwai wanda yake qirqirar halitta ba tare da ya ga samfur a wurin wani ba, sannan ya tayar da ita bayan mutuwarsa?. To ta yaya ake karkatar daku – Ya ku Mushirikai- daga gaskiya zuwa qarya?.**
**(35) Ya kai wannan Manzo ka ce, Shin a cikin abubuwan da kuke haxa Allah da su cikin bauta koma bayan Allah, akwai wanda yake shiryarwa zuwa ga gaskiya? Ka ce musu: "Allah shi ne kaxai wanda yake shiryarwa zuwa ga gaskiya. To shin wanda yake shiryar da mutane zuwa ga gaskiya kuma ya ke kiransu zuwa gare ta shi yafi cancantar ayi masa biyayya ko abubuwan bautarku wanxanda basa iya shiryar da kansu sai dai wani ya shiryar da su?! Me ya sa kuke hukunci da qarya, kuke riya cewa su abokanan tarayyar Allah ne? Allah ya xaukaka daga barin wannan zance naku xaukaka mai girma".**
**(36) Babu abin da mafi yawan Mushirikai suke bi face abin da basu da ilimi a kansa. Babu abin da suke bi sai sai wahami da shakka. Kuma shakka bata maye gurbin ilimi kuma bata wadatarwa a kan komai. Haqiqa Allah ya san abin da suke aikatawa, babu wani abin da yake vuya daga ayyukansu, zai kuma saka musu a kansu.**
**(37) Ba zai tava inganta ba a ce wannan Alqur'anin a qirqire shi, an jingina shi zuwa ga wanin Allah, saboda mutane sun gaza wajen zuwa da irinsa. kuma shi mai gasgatawa ne ga abin da aka saukar na littattafan da suke gabaninsa, mai yin bayani ne na abin da aka dunqule a cikinsu na hukunce-hukuncensu. Don haka babu shakka a kan an saukar da shi ne, daga Ubangijin talikai Maxaukakin Sarki. (38) Ashe wanxannan Mushirikai cewa suke: "Muhammadu (S.A.W) shi ne ya qirqiri wannan Alqur'ani a qashin kansa, kuma ya jingina shi zuwa ga Allah? To ka ce da su - Ya kai wannan Manzo - kana mai mayar musu da martani: "In dai har ni ne, na zo da shi a karan kaina, alhali ni mutum ne irinku, to ku ma ku kawo wata sura irinsa, ku gayyaci duk wanda zaku iya gayyata domin ya taimake ku in har kun kasance masu gaskiya ne cikin abin da kuke yi da'awarsa cewa Alqur'ani qirqirarren littafine na qarya. Ba za su tava iya yin haka ba. Kuma rashin iyawarku –alhali ku masu masana yare ne da fasaha - dalili ne akan cewa Alqur'ani saukakke ne daga wurin Allah. (39) Basu amsa kiran ba, kawai sun yi gaggawar qaryata Alqur'ani tun gabanin su fahimce shi, ko su yi tunani a kansa, kuma tun kafin abin da aka yi musu gargaxinsa na azaba ya tabbata, kuma tabbas hakan ya kusa zuwa. Irin wannan qaryatawar shi ne wanda al'ummun da suka gabata suka yi, sai azaba ta sauka a kansu. Ka yi lura – Ya kai wannan Manzo - da yadda qarshen al'ummu masu qaryata Annabawa ya kasance. Lallai Allah ya halaka su. (40) A cikin Mushrikai akwai wanda zai bada gaskiya da Alqur'ani kafin mutuwarsa, a cikinsu kuma akwai wanda ba zai bayar da gaskiya da shi ba, saboda taurin kai da isa, har ya mutu a haka. Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- shi ne mafi sanin masu zarcewa akan kafircinsu, kuma zai yi musu sakayya akan kafircinsu. (41) Idan har mutanenka – Ya kai wannan Manzo- sun qaryataka, to ka ce musu: "Ladan aiki na nawa ne, kuma zan xauki nauyin aiki na, ku ma ladan aikinku naku ne, uqubarsa ma a kanku zata tsaya. Kun barranta daga abin da nake aikatawa, ni ma na barranta daga uqubar abin da ku ke aikatawa. (42) Daga cikin Mushirikai akwai masu sauraronka – Ya kai Wannan Manzo - idan kana karatun Alqur'ani, ba sauraron karvar gaskiya ko miqa wuya a gare ta ba. Shin kai kana da ikon jiyar da wanda aka karve masa ji ne?! To haka ma ba za ka tava iya shiryar da waxanda suka kurumtar da kansu daga jin gaskiya ba, balle ta shiga hankalinsu.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Allah ne kaxai yake shiryarwa zuwa ga gaskiya, shiriya ta dacewa da karvar ta. 2 - Kwaxaitarwa a kan neman dalilai da hujjoji da shiriya, don samun shiriya da gaskiya da barin wahami da zato. 3 - Babu wanda ya isa ya zo da wani abu koda gwargwadon aya xaya ce, kwatankwacin Alqur'ani mai girma har zuwa ranar alqiyama. 4 - Wautan Mushrikai da qaryatawarsu da abin da basu fahimce shi ba, basu yi tunani a kansa ba.**

ومنهم من ينظر إليك أفأنت تهدي العمي ولو كانوا لا يبصرون
٤٣ إن الله لا يظلم الناس شيئا ولكن الناس أنفسهم
يظلمون ٤٤ ويوم يحشرهم كأن لم يلبثوا إلا ساعة من النهار
يتعارفون بينهم قد خسر الذين كذبوا بلقاء الله وما كانوا
مهتدين ٤٥ وإما نرينك بعض الذي نعدهم أو نتوفينك
فإلينا مرجعهم ثم الله شهيد على ما يفعلون ٤٦ ولكل
أمة رسول فإذا جاء رسولهم قضي بينهم بالقسط وهم
لا يظلمون ٤٧ ويقولون متى هذا الوعد إن كنتم صادقين
٤٨ قل لا أملك لنفسي ضرا ولا نفعا إلا ما شاء الله لكل أمة
أجل إذا جاء أجلهم فلا يستأخرون ساعة ولا يستقدمون ٤٩
قل أرأيتم إن أتاكم عذابه بياتا أو نهارا ماذا يستعجل منه
المجرمون ٥٠ أثم إذا ما وقع آمنتم به آلآن وقد كنتم به
تستعجلون ٥١ ثم قيل للذين ظلموا ذوقوا عذاب الخلد
ربع الحزب ٤٢ هل تجزون إلا بما كنتم تكسبون ٥٢ ۞ ويستنبئونك
أحق هو قل إي وربي إنه لحق وما أنتم بمعجزين ٥٣

**(43)** **Ya kai wannan Manzo a cikin Mushirikai akwai masu kallonka da idanunsu na zahiri ba da basirarsu ba, shin kai zaka iya shiryar da waxanda aka tafiyar da ganinsu? Lallai ba zaka iya haka ba. To haka ma ba zaka iya shiryar da marasa basira ba. (44) Lallai Allah ya tsarkaka daga zaluntar bayinsa, baya zaluntarsu koda da qwayar zarra. Sai dai su ne suke zalunta kawunansu ta hanyar kai kansu ramin halaka saboda ra'ayin riqau ga varna, da girman kai da nuna isa. (45) Ranar da Allah zai tara mutane a ranar alqiyama don ya yi musu hisabi, kamar ka ce basu zauna a rayuwarsu ta duniya da ta barzahu ba face na wani xan lokaci na yini guda kawai ba qari, a lokacin sashensu zai san sashe, amma sanayyar zata katse saboda tsananin abin da za su gani na firgicin alqiyama. Lallai masu qaryata haxuwa da Ubangijinsu a ranar alqiyama sun yi hasara, kuma ga su basu yi imani da ranar tashin alqiyama ba a rayuwarsu ta duniya, ballantana su kuvuta daga hasarar.**

**(46) Kuma da ma zamu nuna maka – Ya kai wannan Manzo- sashe daga cikin abin da muka yi musu alqawari na azaba kafin mutuwarka, ko mu xauki ranka kafin nan, to a duk yanayi biyun makomarsu zuwa gare mu ta ke a ranar alqiyama, sannan kuma Allah yana tsinkayar abin da suka kasance suna aikatawa ne, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma zai saka musu a kan ayyukansu.**

**(47) Kuma kowace al'umma cikin al'ummu da suka gabata suna da Manzo da aka tura musu, idan ya isar musu da saqon da aka umurce shi ya isar musu, suka qaryata shi, sai a yanke hukunci a tsakaninsu da shi da adalci, sai Allah ya kuvutar da shi da falalarsa, ya halaka su da adalcinsa, ba tare da an zalunce su da komai ba cikin sakamakon ayyukansu. (48) Kuma waxannan kafirai za sun riqa cewa – cikin taurin kai da qalubale: "Yaushe ne abin da kuka yi mana alqawari na narkon azaba zai zo, in kun kasance masu gaskiya cikin da'warku?!". (49) Ka ce musu – Ya kai wannan Manzo – "Bana mallakar wata cuta da zan iya cutar da shi da ita, ko in kare shi daga gare ta, haka ma wani amfani da zan amfane shi da shi, ta yaya kuma amfanar da wani ko in cutar da shi?" sai dai abin da Allah ya ga dama, to ta yaya ni zan san abin da Allah ya voye, ya bar wa kansa saninsa? Kowace al'umma ta Allah ya yi mata alqawarin halakarwa tana da lokacinta da aka qayyade mata na halakarta, ba wanda ya san shi sai Allah, don haka in lokacin halakarta ya zo, ba za ya yi jinkiri ba ko a qara.**

**(50) Ya kai wannan Manzo, Ka ce wa waxannan masu neman zuwan azaba da gaggawa – Ya kai wannan Manzo -: "Ku bani labari in har azabar Allah ta zo muku a kowane lokaci na dare ko yini, to me yasa kuke gaggawar zuwan azaba?". (51) A yanzu bayan azabar da aka yi muku alqawari da ita ta faru, zaku yi imani a lokacin da imanin wata rai, wadda bata yi imani ba tun da farko baya amfani. To kuma sai yanzu zaku yi imani, alhali da kun kasance kuna gaggawar neman a saukar muku da azaba, kuna masu qaryatawa?. (52) Sannan bayan an shigar da su cikin azaba kuma suka roqi a fitar dasu daga cikin ta, sai a ce da su: "Ku xanxani azaba ta din-din-din a lahira, shin ashe ba abin da kuka kasance kuna aikatawa na kafirci da savo ba ne ake saka muku da shi ba?".**

**(53) Mushirikai za su riqa tambayarka – Ya kai wannan Manzo – su ce: "Shin wannan azabar da aka yi mana alkawarinta gaskiya ce? Ka ce da su: "Eh, lallai kuwa, wallahi, gaskiya ce, kuma ba zaku kuvuta daga gare ta ba".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Mutum shi yake kai kansa ramin halaka, domin Allah ya tsarkaka daga yin zalunci. 2 - Aikin Manzo shi ne isarwa. Allah kuma shi yake xaukan nauyin yin hisabi da uquba da hikimarsa, kuma yakan iya yi a rayuwar Manzon, ko ya jinkirta sai bayan mutuwarsa. 3 - Amfanarwa da cutarwa suna hannun Allah Maxaukakin Sarki ne, babu wani cikin halitta wanda yake mallakar cutarwa ko amfanarwa a karan kansa ko waninsa. 4 - Imani ba ya amfanar mai yin sa yayin ganin mutuwa.**

وَلَوْ أَنَّ لِكُلِّ نَفْسٍ ظَلَمَتْ مَا فِي ٱلْأَرْضِ لَٱفْتَدَتْ بِهِۦۗ وَأَسَرُّواْ
ٱلنَّدَامَةَ لَمَّا رَأَوُاْ ٱلْعَذَابَۖ وَقُضِيَ بَيْنَهُم بِٱلْقِسْطِ وَهُمْ
لَا يُظْلَمُونَ ﴿٥٤﴾ أَلَآ إِنَّ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِۗ أَلَآ إِنَّ
وَعْدَ ٱللَّهِ حَقٌّ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٥٥﴾ هُوَ يُحْيِۦ وَيُمِيتُ
وَإِلَيْهِ تُرْجَعُونَ ﴿٥٦﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدْ جَآءَتْكُم مَّوْعِظَةٌ
مِّن رَّبِّكُمْ وَشِفَآءٌ لِّمَا فِي ٱلصُّدُورِ وَهُدًى وَرَحْمَةٌ لِّلْمُؤْمِنِينَ
﴿٥٧﴾ قُلْ بِفَضْلِ ٱللَّهِ وَبِرَحْمَتِهِۦ فَبِذَٰلِكَ فَلْيَفْرَحُواْ هُوَ خَيْرٌ مِّمَّا
يَجْمَعُونَ ﴿٥٨﴾ قُلْ أَرَءَيْتُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ لَكُم مِّن رِّزْقٍ
فَجَعَلْتُم مِّنْهُ حَرَامًا وَحَلَٰلًا قُلْ ءَآللَّهُ أَذِنَ لَكُمْۖ أَمْ عَلَى
ٱللَّهِ تَفْتَرُونَ ﴿٥٩﴾ وَمَا ظَنُّ ٱلَّذِينَ يَفْتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلْكَذِبَ
يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَذُو فَضْلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ
لَا يَشْكُرُونَ ﴿٦٠﴾ وَمَا تَكُونُ فِي شَأْنٍ وَمَا تَتْلُواْ مِنْهُ مِن قُرْءَانٍ
وَلَا تَعْمَلُونَ مِنْ عَمَلٍ إِلَّا كُنَّا عَلَيْكُمْ شُهُودًا إِذْ تُفِيضُونَ
فِيهِۚ وَمَا يَعْزُبُ عَن رَّبِّكَ مِن مِّثْقَالِ ذَرَّةٍ فِي ٱلْأَرْضِ وَلَا فِي
ٱلسَّمَآءِ وَلَآ أَصْغَرَ مِن ذَٰلِكَ وَلَآ أَكْبَرَ إِلَّا فِي كِتَٰبٍ مُّبِينٍ ﴿٦١﴾



**(54) Da kowane mai shirka da Allah zai mallaki duk abin da ke cikin qasa na dukiya masu tsada, da ya bayar da su domin ya fanshi kansa daga azabar Allah, inda za a bashi damar ya fanshi kansa da su, Mushirikai zasu voye nadamarsu akan kafircin su yayin da zasu yi ido biyu da azaba a ranar alqiyama, Allah zai yanke musu hukunci na adalci, ba za a zalunce su ba, za a yi musu sakamako ne akan ayyukansu kawai.**

**(55) Ku saurara, haqiqa Allah shi kaxai ne yake da mulkin abin da yake cikin sammai da mulkin abin da yake qassai. Ku saurara, haqiqa alqawarin da Allah ya yi na yi wa kafirai uquba mai aukuwa ne, babu shakka a cikinsa, sai dai mafiya yawansu basu san hakan ba, don haka suke shakka.**

**(56) Allah maxaukakin Sarki shi ne ke tayar da matattu, ya kashe rayayyu, kuma gare shi ne shi kaxai za a mayar da ku a ranar alqiyama, sai ya saka muku akan ayyukanku.**

**(57) Ya ku mutane, haqiqa Alqur'ani ya zo muku, a cikinsa akwai tunatarwa da kwaxaitarwa da tsoratarwa, kuma shi waraka ne ga abin da ke cikin zukata na cutar shakka da kokwanto, kuma shiriya ne zuwa tafarkin gaskiya, kuma a cikinsa akwai jin qai ga muminai, don haka su ne masu amfana da shi.**

**(58) Ka ce wa mutane – Ya kai wannan Manzo -: "Abin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo muku da shi na Alqur'ani falala ne daga Allah zuwa gare ku, kuma rahama ne daga gare shi zuwa gare ku. Don haka, da wannan falalar ta Allah a kanku da rahamarsa a gare ku na saukar da wannan Alqur'anin ya dace ku yi farin ciki, ba da waninsu ba. Domin abin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo musu da shi daga Ubangijinsa shi ya fi musu alheri sama da duk wani abin da suke tarawa na kayan duniya mai gushewa.**

**(59) Ka ce wa waxannan Mushirikai – Ya kai wannan Manzo -: "Ku bani labari dangane da ni'imar da Allah ya yi muku na saukar da arziki, amma sai kuka yi aiki da shi a kan son zukatanku, kuka haramta wani sashe, kuka halatta wani sashe. To ka ce musu: "Shin Allah ne ya yi muku izini cikin halatta abin da kuka halatta, da haramta abin da kuka haramta, kodai ku ne kuke qirqirar qarya ku jingina masa?!".**

**(60) Masu qirqirar qarya ga Allah me suke zaton zai faru da su ne a ranar alqiyama?! Shin suna zaton za a gafarta musu ne?! Faufau har abada!. Haqiqa Allah mai matukar falala ne akan mutane ta hanyar jinkirta musu, da rashin gaggauta musu uquba, amma mafiya yawansu masu butulce wa ni'imomin da Allah ya yi musu ba sa nuna godiyarsu a kai.**

**(61) Babu wani sha'ani da zaka kasance a cikinsa –Ya kai wannan Manzo-, haka ma babu wani abin da zaka karanta na Alqur'ani, haka ma babu wani abin da zaku aikata na aiki – Ku Muminai- face sai mun kasance muna kallonku, muna sane da ku, muna jin ku, tun daga lokacin da kuka fara aikin, har zuwa lokacin da kuke kutsawa cikinsa. Babu wani abu daidai da qwayar zarra da yake vuya daga sanin Ubangijinka a sama ko a qasa, haka babu wani abi da yake qasa da qwayar zarra, ko ya fi ta girma face yana rubuce a cikin wani littafi bayyananne, wanda baya barin wani abu qarami ko babba face sai ya qididdige shi.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Girman abin da ya ke jiran mai shirka da Allah na azaba, har zasu yi burin ina ma da za su iya tunkuxe shi ta hanyar bayar da duk abin da yake qasa, amma ba za a karva ba har abada. 2 - AlQur'ani waraka ne ga Muminai daga cututtukan sha'awa da cututtukan shubuhohi, saboda abin da ke cikin sa na shiriya da dalilai na hankali da na nassi.**

**3 - Ya dace Muminai su yi farin ciki da ni'mar Musulunci da Imani ne, ba da waninsu ba na dukiyar duniya ba.**

**4 - Bayanin yadda Allah yake bibiyar bayinsa da ayyukansu da abin da suke saqawa a zuciyarsu da niyyoyinsu.**

أَلَآ إِنَّ أَوۡلِيَآءَ ٱللَّهِ لَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ ٦٢
ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَكَانُواْ يَتَّقُونَ ٦٣ لَهُمُ ٱلۡبُشۡرَىٰ
فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِۚ لَا تَبۡدِيلَ لِكَلِمَٰتِ
ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ٦٤ وَلَا يَحۡزُنكَ قَوۡلُهُمۡۘ إِنَّ
ٱلۡعِزَّةَ لِلَّهِ جَمِيعًاۚ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٦٥ أَلَآ إِنَّ لِلَّهِ
مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِۗ وَمَا يَتَّبِعُ ٱلَّذِينَ
يَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ شُرَكَآءَۚ إِن يَتَّبِعُونَ إِلَّا ٱلظَّنَّ
وَإِنۡ هُمۡ إِلَّا يَخۡرُصُونَ ٦٦ هُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ
ٱلَّيۡلَ لِتَسۡكُنُواْ فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبۡصِرًاۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَسۡمَعُونَ ٦٧ قَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدٗاۗ
سُبۡحَٰنَهُۥۖ هُوَ ٱلۡغَنِيُّۖ لَهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ
إِنۡ عِندَكُم مِّن سُلۡطَٰنِۭ بِهَٰذَآۚ أَتَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ
مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٦٨ قُلۡ إِنَّ ٱلَّذِينَ يَفۡتَرُونَ عَلَى ٱللَّهِ ٱلۡكَذِبَ
لَا يُفۡلِحُونَ ٦٩ مَتَٰعٞ فِي ٱلدُّنۡيَا ثُمَّ إِلَيۡنَا مَرۡجِعُهُمۡ ثُمَّ
نُذِيقُهُمُ ٱلۡعَذَابَ ٱلشَّدِيدَ بِمَا كَانُواْ يَكۡفُرُونَ ٧٠



**(62) Ku Saurara!. Haqiqa waliyyan Allah babu tsoro a kansu cikin abin da suke fuskantarsu na abubuwan tsoro na alqiyama, kuma baza su yi baqin ciki ba a kan abin da ya kuvuce musu na rabon duniya.**

**(63) Waxannan waliyyai su ne waxanda suka siffantu da imani da Allah da Manzon Allah (S.A.W), sannan suka kasance suna jin tsoron Allah ta hanyar aiwatar da umarninsa da nisantar haninsa.**

**(64) Suna da albishiri daga Ubangijinsu a duniya na abin da zai faranta musu rai, ta hanyar kyakkyawan mafarki ko yabon mutane a gare su, kuma suna da albishir daga Mala’iku a yayin karvar rayukansu, haka nan bayan mutuwa da kuma ranar alqiyama. Babu canji cikin abin da Allah ya yi musu alqawarinsa. Wannan sakamako shi ne babban rabo, saboda abin da ke ciki na samun biyan buqata da kuvuta daga abin tsoro.**

**(65) Ya kai wannan Manzon kar ka yi baqin ciki dangane da abin da waxannan suke faxa na suka da zambo akan addininka. Lallai buwaya da galaba duk na Allah ne. Babu abin da yake gagararsa. Shi ne mai jin maganganunsu, kuma masanin ayyukansu, kuma zai yi musu sakayya a kai.**

**(66) Ku Saurara! Haqiqa Allah shi ne kaxai mamallakin wanxanda suke sammai da waxanda suke qassai. To wane abu mushirikai masu bauta wa wanin Allah suke bi?! Babu abin da suke bi alal- haqiqa sai shakka, babu abin da suke yi face qarya cikin jingina wa Allah abokan tarayya da suke yi ga Allah, Allah ya xaukaka daga barin wannan zance nasu xaukaka mai girman gaske.**

**(67) Allah ne kaxai wanda ya sanya muku dare, domin ku huta a cikinsa daga zirga -zirga da gajiya, kuma ya saka muku yini mai haske, domin ku yi aikin da zai jawo muku amfani a rayuwarku a cikinsa. Lallai a cikin yin haka akwai dalilai bayyanannu ga mutane masu ji, ji na izina da karvar gaskiya.**

**(68) Wasu vangare na mushirikai sun ce: “Allah ya xauki Malaiku a matsayin 'ya'ya mata - Allah ya tsarkaka daga barin wannan zance nasu - Ai Shi Maxaukakin Sarki wadatacce ne ga barin halittunsa gaba xaya, Shi ne mamallakin duk abin da ke sama, da duk abin da ke qasa. Ku Mushirikai ba ku da wani dalili akan wannan zance naku! Shin haka zaku riqa faxawa Allah wannan mummunan zance, kuna jingina shi ga Allah – yayin da kuke jingina masa ‘ya’ya mata – maganar da baku san haqiqaninta ba, kuma bata da wata hujja!.**

**(69) Ka ce musu – Ya kai wannan Manzo- haqiqa masu qirqirar karya ta hanyar jinginawa Allah xa, ba zasu samu biyan buqatarsu ba, kuma baza su quvuta daga abin da suke tsoro ba!.**

**(70) Don haka kar ku ruxu da abin da suke jin daxi da shi na kayan daxin duniya da ni'imominta, domin jin daxi ne xan kaxan, kuma mai gushewa, sannan makomarsu ranar alqiyama zuwa garemu take, kuma zamu xanxana musu azaba mai tsanani, saboda kafircinsu da Allah da qaryatawarsu ga Manzonsa.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Walittakar Allah tana kasancewa ne ga wanda yayi imani da shi, ya bi umarninsa, ya nisanci haninsa, ya yi biyayya ga Manzonsaa (S.A.W). Kuma waliyyan Allah su ne masu aminci a ranan lahira, kuma suna da albishir a duniya imma ta hanyar kakkyawan mafarki, ko kuma yayin mutuwa. 2 - Buwaya gaba xaya ta Allah ce, shi kaxai, domin shi ne mamallakin komai. Kuma duk wani abin da aka bauta masa koma bayan Allah, to ba gaskiya ba ne.**

**3 - Qwaxaitarwa akan yin tunani cikin halittar Allah, domin hakan yana kaiwa zuwa ga imani da Allah da qaxaita shi da bauta. 4 - Haramcin yi wa Allah qarya da bayanin cewa duk wanda ya aikata haka ba zai tsira ba. Kuma yana daga cikin mafi girman qarya a jingina xa ga Allah Maxaukakin Sarki.**

نصف الحزب ٢٢

۞ وَٱتۡلُ عَلَيۡهِمۡ نَبَأَ نُوحٍ إِذۡ قَالَ لِقَوۡمِهِۦ يَٰقَوۡمِ إِن كَانَ كَبُرَ
عَلَيۡكُم مَّقَامِي وَتَذۡكِيرِي بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَعَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلۡتُ
فَأَجۡمِعُوٓاْ أَمۡرَكُمۡ وَشُرَكَآءَكُمۡ ثُمَّ لَا يَكُنۡ أَمۡرُكُمۡ عَلَيۡكُمۡ غُمَّةٗ ثُمَّ
ٱقۡضُوٓاْ إِلَيَّ وَلَا تُنظِرُونِ ٧١ فَإِن تَوَلَّيۡتُمۡ فَمَا سَأَلۡتُكُم مِّنۡ أَجۡرٍۖ
إِنۡ أَجۡرِيَ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِۖ وَأُمِرۡتُ أَنۡ أَكُونَ مِنَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ٧٢
فَكَذَّبُوهُ فَنَجَّيۡنَٰهُ وَمَن مَّعَهُۥ فِي ٱلۡفُلۡكِ وَجَعَلۡنَٰهُمۡ خَلَٰٓئِفَ
وَأَغۡرَقۡنَا ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَاۖ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُنذَرِينَ
٧٣ ثُمَّ بَعَثۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِۦ رُسُلًا إِلَىٰ قَوۡمِهِمۡ فَجَآءُوهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ
فَمَا كَانُواْ لِيُؤۡمِنُواْ بِمَا كَذَّبُواْ بِهِۦ مِن قَبۡلُۚ كَذَٰلِكَ نَطۡبَعُ عَلَىٰ قُلُوبِ
ٱلۡمُعۡتَدِينَ ٧٤ ثُمَّ بَعَثۡنَا مِنۢ بَعۡدِهِم مُّوسَىٰ وَهَٰرُونَ إِلَىٰ فِرۡعَوۡنَ
وَمَلَإِيْهِۦ بِـَٔايَٰتِنَا فَٱسۡتَكۡبَرُواْ وَكَانُواْ قَوۡمٗا مُّجۡرِمِينَ ٧٥
فَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلۡحَقُّ مِنۡ عِندِنَا قَالُوٓاْ إِنَّ هَٰذَا لَسِحۡرٞ مُّبِينٞ ٧٦
قَالَ مُوسَىٰٓ أَتَقُولُونَ لِلۡحَقِّ لَمَّا جَآءَكُمۡۖ أَسِحۡرٌ هَٰذَا وَلَا يُفۡلِحُ
ٱلسَّٰحِرُونَ ٧٧ قَالُوٓاْ أَجِئۡتَنَا لِتَلۡفِتَنَا عَمَّا وَجَدۡنَا عَلَيۡهِ ءَابَآءَنَا
وَتَكُونَ لَكُمَا ٱلۡكِبۡرِيَآءُ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا نَحۡنُ لَكُمَا بِمُؤۡمِنِينَ ٧٨



**(71) Ya kai wannan Manzo, ka ba waxannan mushirikai masu qaryata Annabawa labarin Annabi Nuhu (S.A.W), yayin da ya ce wa mutanensa: "Ya ku mutane na, idan zamana a tsakanin ku ya yi muku nauyi, kuma wa'azi da tunatarwar da nake yi da ayoyin Allah sun saka ku cikin qunci, har kuna nufin kashe ni, to ni na dogara ne ga Allah shi kaxai wajen rushe makircinku. Don haka, ku yi ta tsara sha'aninku, kuma ku yi ta shirin halaka ni, kuma ku kira abubuwan bautarku don ku nemi taimakonsu, sannan kuma kar ku yi wannan makircin a sirrance a voye, kuma bayan kun shirya yadda zaku kashe ni ku zartar da abin da kuka qulla a zukatanku, kuma kar ku saurara min ko da qanqanin lokaci ne.**

**(72) Idan kun juyawa kira na baya, to ku sani cewa ban tava tambayarku wani lada ba akan isar muku da saqon Allah. Ladana baya wajen kowa sai Allah, ku ba da gaskiya da ni, ko ku qi ba da gaskiya, ni dai Allah ya umurce ni in kasance cikin masu qanqan da kai a gare shi, ta hanyar xa'a da aiki nagari.**

**(73) Sai mutanensa suka qaryata shi, basu gaskata shi ba, sai muka tseratar da shi, shi da Muminai waxanda suka kasance tare da shi a cikin jirgin ruwa, muka sa su suka maye gurbin magabatansu, kuma muka halaka waxanda suka qaryata abin da ya zo da shi na ayoyi da hujjoji, muka halaka su da ruwan xufana. Ka yi tunani - Ya kai wannan Manzo- a kan yadda qarshen lamarin mutanen da Annabi Nuhu (A.S) ya yi musu gargaxi, suka qi yin imani ya kasance. (74) Sannan bayan wani zango na zamani sai muka tayar da wasu Manzanni bayan Annabi Nuhu zuwa ga mutanensu. Manzannin suka kawo wa mutanensu dalilai da hujjoji, amma basu ga damar su yi imani ba, saboda zarcewarsu akan qaryata Manzanni, sai Allah ya rufe zukatansu. Irin wannan rufewar da muka yi akan zukatan mutanen Annabawan da suka gabata, haka zamu yi akan zukatan kafirai masu qetare iyakokin Allah, ta hanyan kafirci a kowane zamani da lokaci. (75) Sannan bayan wani zango na zamani bayan waxannan Manzanni, sai muka tura Annabi Musa da xan 'uwansa Annabi Haruna zuwa ga Fir'auna, sarkin Misra da manya manyan mutanensa. Mun tura su da hujjoji masu tabbatar da gaskiyar manzancinsu, amma sai Fir'auna da mutanensa suka yi girman kai, suka qi yin imani da abin da suka zo musu da shi, sai suka kasance mutane masu laifi, saboda kafircinsu da Allah da qaryatawar su ga Manzanni.**

**(76) Yayin da Annabi Musa da Annabi Haruna (A.S) suka zo wa Fir'auna da manyan mutanensa da addinin gaskiya, sai suka cewa ayoyin da suka zo da su, waxanda suke nuna gaskiyar a bin da Annabi Musa ya zo da shi, sai suka ce, "Wannan ai sihiri ne bayyananne, wanda ba a voye yake ba".**

**(77) Sai Annabi Musa ya ce musu, yana mai musu inkari: "Yanzu haka zaku kira gaskiyar da ta zo muku, da sihiri?!,. Ba haka lamarin yake ba! Ba sihiri ba ne, saboda ni na san mai yin sihiri baya rabauta har abada, to kuma ta yaya zan yi shi?" .**

**(78) Sai mutanen Fir'auna suka mayar da martani ga Annabi Musa (A.S) suna masu cewa: "Shin ka zo mana da wannan sihirin ne domin ka kawar damu daga abin da muka samu iyayenmu a kai na addini, kuma domin mulki ya zama na ku, kai da xan 'uwanka? Mu samsam baza mu tava yarda da kai Musa da xan uwanka Haruna ba, cewa ku manzanni ne da aka turo mana.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Matsayin mumini wajen fuskantar abokan gabansa shi ne, dogaro ga Allah. 2 - Zarcewa akan kafirci da qaryata Manzanni yana haifar da rufe zukata su kasa yin imani har abada. 3 - Halin maqiya Manzanni iri xaya ne. Su a koyaushe suna siffanta shiriya da cewa sihiri ce ko qarya. 4 - Lallai mai sihiri ba zai tava rabauta da alheri ba har abada.**

وَقَالَ فِرۡعَوۡنُ ٱئۡتُونِي بِكُلِّ سَٰحِرٍ عَلِيمٖ ٧٩ فَلَمَّا جَآءَ ٱلسَّحَرَةُ
قَالَ لَهُم مُّوسَىٰٓ أَلۡقُواْ مَآ أَنتُم مُّلۡقُونَ ٨٠ فَلَمَّآ أَلۡقَوۡاْ قَالَ
مُوسَىٰ مَا جِئۡتُم بِهِ ٱلسِّحۡرُۖ إِنَّ ٱللَّهَ سَيُبۡطِلُهُۥٓ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُصۡلِحُ
عَمَلَ ٱلۡمُفۡسِدِينَ ٨١ وَيُحِقُّ ٱللَّهُ ٱلۡحَقَّ بِكَلِمَٰتِهِۦ وَلَوۡ كَرِهَ
ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٨٢ فَمَآ ءَامَنَ لِمُوسَىٰٓ إِلَّا ذُرِّيَّةٞ مِّن قَوۡمِهِۦ عَلَىٰ
خَوۡفٖ مِّن فِرۡعَوۡنَ وَمَلَإِيْهِمۡ أَن يَفۡتِنَهُمۡۚ وَإِنَّ فِرۡعَوۡنَ لَعَالٖ
فِي ٱلۡأَرۡضِ وَإِنَّهُۥ لَمِنَ ٱلۡمُسۡرِفِينَ ٨٣ وَقَالَ مُوسَىٰ يَٰقَوۡمِ إِن
كُنتُمۡ ءَامَنتُم بِٱللَّهِ فَعَلَيۡهِ تَوَكَّلُوٓاْ إِن كُنتُم مُّسۡلِمِينَ ٨٤
فَقَالُواْ عَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلۡنَا رَبَّنَا لَا تَجۡعَلۡنَا فِتۡنَةٗ لِّلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ
٨٥ وَنَجِّنَا بِرَحۡمَتِكَ مِنَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٨٦ وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰ
وَأَخِيهِ أَن تَبَوَّءَا لِقَوۡمِكُمَا بِمِصۡرَ بُيُوتٗا وَٱجۡعَلُواْ بُيُوتَكُمۡ
قِبۡلَةٗ وَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَۗ وَبَشِّرِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٨٧ وَقَالَ مُوسَىٰ
رَبَّنَآ إِنَّكَ ءَاتَيۡتَ فِرۡعَوۡنَ وَمَلَأَهُۥ زِينَةٗ وَأَمۡوَٰلٗا فِي ٱلۡحَيَوٰةِ
ٱلدُّنۡيَا رَبَّنَا لِيُضِلُّواْ عَن سَبِيلِكَۖ رَبَّنَا ٱطۡمِسۡ عَلَىٰٓ أَمۡوَٰلِهِمۡ
وَٱشۡدُدۡ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ فَلَا يُؤۡمِنُواْ حَتَّىٰ يَرَوُاْ ٱلۡعَذَابَ ٱلۡأَلِيمَ ٨٨



**(79) Fir'auna ya ce da mutanensa: "Ku kawo min duk wani matsafi gwani wanda ya qware a cikin tsafi".**

**(80) Yayin da suka zo da matsafa wajen Fir'auna sai Annabi Musa (S.A.W) ya ce, yana mai tabbaci zai yi nasara a kansu: "Ya ku waxannan matsafa, ku jefo duk abin da za ku iya jefawa".**

**(81) Yayin da suka jefa abin da suka zo da shi na tsafi da sihiri sai Annabi Musa (S.A.W) ya ce musu: W"annan abin da kuka zo da shi tsafi ne, Allah zai mayar da abin da kuka yi vatacce maras tasiri. Haqiqa ku masu varna ne a bayan qasa saboda wannan tsafi da kuke yi. Kuma Allah baya gyara aikin duk wanda ya kasance mavarnaci".**

**(82) Kuma Allah zai tabbatar da gaskiya, zai tabbatar da ita da kalmominsa da ya qaddara, da abin da yake cikin kalmominsa na shari'a, koda kuwa kafirai masu laifi mabiya Fir'auna sun qi.**

**(83) Mutanen sun zarce akan kawar da kansu, har ma babu waxanda suka bayar da gaskiya da Annabi Musa (S.A.W) da abin da ya zo da shi, na ayoyi bayyanannu, da dalilai na fili, sai wasu samari cikin mutanensa bani Isra'ila tare da tsoron fir'auna da manya-manya mutanensa, kar su juyar da su daga imaninsu, saboda azabar da za su gana musu in lamarinsu ya bayyana. Lallai Fir'auna mai girman kai ne, mai mulkin kama-karya a kan Misra da mutanenta, kuma lallai yana cikin masu wuce gona da iri cikin kafirci da kisan kyashi, da azabtarwa ga bani isra'ila.**

**(84) Annabi Musa (S.A.W) ya ce wa mutanensa: "Ya ku mutanena, in har kun yi imani da Allah, imani na gaskiya, to ku dogara da Allah shi kaxai, in har ku musulmai ne, saboda dogaro ga Allah shi ne zai kawar muku da cuta, ya jawo muku alheri.**

**(85) Sai suka amsa wa Annabi Musa (S.A.W), suka ce: "Mun dogara ga Allah shi kaxai. Ya Ubangijinmu kada ka xora azzalumai a kanmu, balle su fitine mu kan barin addininmu, da azabtarwa da kisa da zaburar da mutane a kanmu.**

**(86) Ka tseratar da mu da jin qan ka – Ya Ubangijinmu - daga hannun kafiran mutanen Fir'auna, domin haqiqa sun bautar da mu, sun cutar da mu da azabtarwa da kisa.**

**(87) Mun yi wahayi ga Annabi Musa da xan 'uwansa Annabi Haruna (S.A.W) cewa ku zavar wa mutanenku wasu gidaje don bautawa Allah shi kaxai, ku mayar da gidajenku su fuskanci alqibla (Wato Baitul Maqdis), ku yi sallah cikakkiya, kuma -kai Annabi Musa- ka yi wa mutanenka albishir da nasarar Allah da goyon baya a gare su, da kuma halaka maqiyansu, da kuma gadar musu da mulkin qasar.**

**(88) Annabi Musa (S.A.W) ya ce: "Ya Ubangijinmu haqiqa ka bai wa Fir'auna da manyan mutanensa abubuwa qawa na duniya, ka ba su dukiya a wannan rayuwa ta duniya, amma basu gode maka akan abin da ka basu ba, sai dai ma suka yi amfani da ita wajen vatar da mutane daga bin hanyarka. Ya Ubangijinmu ka shafe dukiyarsu, ka lalata su, ka sanya zukatansu su qeqashe, baza su yi imani ba, har sai sun ga azaba mai raxaxi, a lokacin da imaninsu ba zai amfane su ba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yarda da Allah da taimakonsa da dogaro da shi ya dace ya zama cikin siffofin mumini mai qarfin imani.**

**2 - Bayanin mahimmancin Addu'a da kasancewarta cikin siffofin masu dogaro ga Allah (wato tawakkali).**

**3 - Tabbatar da mahimmancin sallah da wajabcin tsayar da ita cikin addinan da aka saukar da su daga sama a kowane irin yanayi.**

**4 - Hallacin yin mummunan addu'a a kan azzalumi.**

قَالَ قَدْ أُجِيبَت دَّعْوَتُكُمَا فَٱسْتَقِيمَا وَلَا تَتَّبِعَآنِّ سَبِيلَ
ٱلَّذِينَ لَا يَعْلَمُونَ ﴿٨٩﴾ ۞ وَجَٰوَزْنَا بِبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ٱلْبَحْرَ فَأَتْبَعَهُمْ (ثلاثة أرباع الحزب ٢٢)
فِرْعَوْنُ وَجُنُودُهُۥ بَغْيًا وَعَدْوًا ۖ حَتَّىٰٓ إِذَآ أَدْرَكَهُ ٱلْغَرَقُ
قَالَ ءَامَنتُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱلَّذِىٓ ءَامَنَتْ بِهِۦ بَنُوٓا۟ إِسْرَٰٓءِيلَ
وَأَنَا۠ مِنَ ٱلْمُسْلِمِينَ ﴿٩٠﴾ ءَآلْـَٰٔنَ وَقَدْ عَصَيْتَ قَبْلُ وَكُنتَ
مِنَ ٱلْمُفْسِدِينَ ﴿٩١﴾ فَٱلْيَوْمَ نُنَجِّيكَ بِبَدَنِكَ لِتَكُونَ لِمَنْ
خَلْفَكَ ءَايَةً ۚ وَإِنَّ كَثِيرًا مِّنَ ٱلنَّاسِ عَنْ ءَايَٰتِنَا لَغَٰفِلُونَ
﴿٩٢﴾ وَلَقَدْ بَوَّأْنَا بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ مُبَوَّأَ صِدْقٍ وَرَزَقْنَٰهُم مِّنَ
ٱلطَّيِّبَٰتِ فَمَا ٱخْتَلَفُوا۟ حَتَّىٰ جَآءَهُمُ ٱلْعِلْمُ ۚ إِنَّ رَبَّكَ يَقْضِى
بَيْنَهُمْ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُوا۟ فِيهِ يَخْتَلِفُونَ ﴿٩٣﴾ فَإِن كُنتَ فِى شَكٍّ
مِّمَّآ أَنزَلْنَآ إِلَيْكَ فَسْـَٔلِ ٱلَّذِينَ يَقْرَءُونَ ٱلْكِتَٰبَ مِن
قَبْلِكَ ۚ لَقَدْ جَآءَكَ ٱلْحَقُّ مِن رَّبِّكَ فَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُمْتَرِينَ ﴿٩٤﴾
وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلَّذِينَ كَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَتَكُونَ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ
﴿٩٥﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ حَقَّتْ عَلَيْهِمْ كَلِمَتُ رَبِّكَ لَا يُؤْمِنُونَ ﴿٩٦﴾
وَلَوْ جَآءَتْهُمْ كُلُّ ءَايَةٍ حَتَّىٰ يَرَوُا۟ ٱلْعَذَابَ ٱلْأَلِيمَ ﴿٩٧﴾



89 Allah Ya ce: “Haqiqa na amsa addu'arku –Ya kai Musa da Haruna- a kan Fir'auna da manyan mutanensa. Saboda haka ku tabbata akan addininku, kada ku karkata zuwa ga bin tafarkin jahilai waxanda basu san tafarkin gaskiya ba.

90 Kuma Mun sauwaqe wa Bani Israi'la tsallake teku bayan Mun raba shi gida biyu, har sai da suka qetare shi cikin aminci, sai Fir'auna ya biyo bayansu, shi da rundunarsa, saboda zalunci da shishshigi, sai da tekun ya haxe da shi, ya nutse a ciki, ya xebe qauna daga rayuwa, sannan ya ce: Na ba da gaskiya cewa babu abin bautawa da gaskiya sai wannan da Bani Isra'ila suka ba da gaskiya da shi, kuma ina cikin masu miqa wuya a gare shi.

Sai dai, da yake tuba yayin ganin mutuwa ba’a karva, don haka sai Allah Maxaukakin Sarki ya ce:

91 Yanzu ne zaka yi imani bayan ka xebe qauna daga rayuwa?! Alhali ka sava wa Allah –Ya kai Fir'auna- kafin a saukar da azaba, ta hanyar kafirce masa, da kange hanyarsa ga mutane, kuma ka kasance cikin mavarnata, ta hanyar vacewa da vatar da waninka!.

92 Yau zamu fitar da kai –Ya kai Fir'auna- daga teku, mu xora ka akan tudun qasa, domin masu zuwa bayanka su xaui izina da kai. Kuma lallai da yawa cikin mutane masu rafkannuwa ne dangane da hujjojinmu da dalilan ikonmu, ba sa tunani a cikinsu.

93 Kuma lallai mun saukar da bani Isra'ila a masauki mai kyau, abin yarda, cikin biranen Sham masu albarka, kuma mun azurta su da daxaxan abubuwan halal, amma basu tashi yin savani cikin lamarin addininsu ba sai da Alqur'ani mai gaskata abin da suka karanta a Attaura, na siffofin Annabi Muhammadu (S.A.W). Yayin da suka yi inkarin gaskiyar da ta zo musu, sai aka qwace musu qasashensu. Lallai Ubangijinka -Ya kai wannan Manzo- zai yi hukunci a tsakaninsu ranar alqiyama akan abin da suka kasance suna savani a kai, sai ya sakawa mai gaskiya da mai qarya a cikinsu da abin da ya cancanci kowannensu.

94 Amma fa in ka kasance –Ya kai wannan Manzo- cikin shakka da ruxu dangane da haqiqanin abin da muka saukar zuwa gare ka na Alqur'ani, to ka tambayi waxanda suka yi imani cikin Yahudawan da suke karanta Attaura, da Nasaran da suke karanta Injila, zasu baka labarin cewa abin da aka saukar maka gaskiya ne, saboda abin da suka samu na siffofinsa a littattafansu. Lallai gaskiyar da babu shakku a cikinta ta zo maka daga Ubangijinka, don haka kada ka zama cikin masu shakka.

95 kada ka kasance cikin masu qaryata hujjojin Allah da dalilansa sai ka zama cikin hasararru, waxanda suka yi hasarar kawunansu, ta hanyar shigar da kansu hanyoyin halaka saboda kafircinsu. An yi wannan gargaxi ne domin bayyana haxarin shakku ne da qaryata Allah, in ba haka ba, ai Annabi an ba shi kariya (wato ma'sumi ne) daga wani abu irin wannan.

96 Lallai waxanda hukuncin Allah ya tabbata a kansu cewa zasu mutu akan kafirci sakamakon zarcewarsu a kai, to har abada ba zasu tava ba da gaskiya ba.

97 Ko da kuwa dukkanin hujjoji na Shari'ah da na halitta za su zo musu, har sai sun ga azaba mai raxaxi, sannan za su ba da gaskiya a yayin da imani ba zai amfane su ba.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Wajabcin tabbata akan addini da rashin bin tafarkin masu laifi (mujrimai).

2 - Ba a karvan tuban wanda ransa ta zo maqogwaro ko wanda ya yi ido huxu da azaba.

3 - Lallai Yahudawa da Nasara suna da masaniya dangane da siffofin Annabi (S.A.W), ammai dai girman kai ne da taurin kunne suka hana su bayar da gaskiya da shi.

فَلَوْلَا كَانَتْ قَرْيَةٌ ءَامَنَتْ فَنَفَعَهَآ إِيمَٰنُهَآ إِلَّا قَوْمَ يُونُسَ
لَمَّآ ءَامَنُوا۟ كَشَفْنَا عَنْهُمْ عَذَابَ ٱلْخِزْىِ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا
وَمَتَّعْنَٰهُمْ إِلَىٰ حِينٍ ٩٨ وَلَوْ شَآءَ رَبُّكَ لَءَامَنَ مَن فِى ٱلْأَرْضِ
كُلُّهُمْ جَمِيعًا ۚ أَفَأَنتَ تُكْرِهُ ٱلنَّاسَ حَتَّىٰ يَكُونُوا۟ مُؤْمِنِينَ
٩٩ وَمَا كَانَ لِنَفْسٍ أَن تُؤْمِنَ إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۚ وَيَجْعَلُ ٱلرِّجْسَ
عَلَى ٱلَّذِينَ لَا يَعْقِلُونَ ١٠٠ قُلِ ٱنظُرُوا۟ مَاذَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضِ ۚ وَمَا تُغْنِى ٱلْءَايَٰتُ وَٱلنُّذُرُ عَن قَوْمٍ لَّا يُؤْمِنُونَ
١٠١ فَهَلْ يَنتَظِرُونَ إِلَّا مِثْلَ أَيَّامِ ٱلَّذِينَ خَلَوْا۟ مِن قَبْلِهِمْ ۚ
قُلْ فَٱنتَظِرُوٓا۟ إِنِّى مَعَكُم مِّنَ ٱلْمُنتَظِرِينَ ١٠٢ ثُمَّ نُنَجِّى
رُسُلَنَا وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ۚ كَذَٰلِكَ حَقًّا عَلَيْنَا نُنجِ ٱلْمُؤْمِنِينَ ١٠٣
قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِن كُنتُمْ فِى شَكٍّ مِّن دِينِى فَلَآ أَعْبُدُ ٱلَّذِينَ
تَعْبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَٰكِنْ أَعْبُدُ ٱللَّهَ ٱلَّذِى يَتَوَفَّىٰكُمْ ۖ وَأُمِرْتُ
أَنْ أَكُونَ مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ١٠٤ وَأَنْ أَقِمْ وَجْهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفًا
وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُشْرِكِينَ ١٠٥ وَلَا تَدْعُ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا
يَنفَعُكَ وَلَا يَضُرُّكَ ۖ فَإِن فَعَلْتَ فَإِنَّكَ إِذًا مِّنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٠٦



**(98) Ba a tava samun wata alqarya cikin alqaryun da muka tura musu manzanni sun yi imanin da aka yi la'akari da shi ba, har ya amfane su, saboda sun yi shi kafin su yi ido huxu da azaba, sai mutanen Annabi Yunusa (A.S), yayin da suka yi imani na gaskiya, sai muka yaye musu azabar qasqanci da wulaqanci a rayuwar duniya, kuma muka ba su jin daxi na xan wani lokaci kaxan, zuwa qarshen ajalinsu.**

**(99) Da Ubangijinka –Ya kai wannan Manzo- ya ga damar duk wanda ke doron qasa ya bada gaskiya, da duka sun yi imani, ammai bai ga damar haka ba, saboda wata hikima, Shi yake vatar da wanda ya ga dama da adalcinsa, ya shiryar da wanda ya ga dama da falalarsa, don haka kai ba zaka iya tilasta wa mutane su zama muminai ba, saboda datar da su zuwa imani yana hannun Allah ne shi kaxai.**

**(100) Kuma bai yiwuwa ga wata rai a karan kanta ta ba da gaskiya face sai da izinin Allah, Imani ba shi yiwuwa sai da ganin damarsa, don haka kar ka halakar da kanka cikin baqin ciki akan basu yi imani ba. Allah yana sanya azaba da wulaqanci a kan waxanda ba sa fahimtar hujjojinsa da abubuwan da ya umarta da waxanda ya hana.**

**(101) Ya kai wannan Manzo ka cewa Mushirikan da suke tambayarka ka kawo musu ayoyi: "Ku yi tunani, mene ne a cikin sammai da qassai na dalilai masu tabbatar da kaxaituwar Allah da ikonsa. Kuma amfanin me saukar da ayoyi da hujjoji da manzanni zai yi ga mutanen da basu da shirin su yi imani, saboda zarcewarsu akan kafirci!. (102) Me waxannan Masu qaryata Manzannin suke jira ban da irin abubuwan da Allah ya saukar da su akan al'ummu masu qaryata Manzanni da suka gabata?! Ka ce musu – Ya kai wannan Manzo-: "Ku jira azabar Allah. Lallai ni ma ina nan tare daku cikin masu jiran alqawarin Ubangiji na".**

**(103) Sannan zamu saukar da azaba a kansu, kuma mu kuvutar da Manzanninmu, mu kuvutar da waxanda suka yi imani da su. Abin da ya auku ga mutanensu ba zai shafe su ba. Kamar yadda muka tseratar da waxancan Manzanni da waxanda suka yi imani da su, haka zamu kuvutar da Manzon Allah da waxanda suka ba da gaskiya da shi, kuvutarwa ta gaskiya, haqqi ne tabbatacce a kanmu.**

**(104) Ya kai wannan Manzo ka ce: "Ya ku mutane, in har kuna shakka dangane da addini na, wanda nake kiranku zuwa gare shi, wato addinin kaxaita Allah da bauta (Tauhidi), to ni fa ina da tabbacin vacin addininku, don haka ba zan bi shi ba, ba zan bauta wa waxanda kuke bautawa ba koma bayan Allah, sai dai in bauta wa Allah wanda shi yake xaukan ran ku (ya kashe ku), kuma shi ya yi min umarni da in zama cikin muminai masu kaxaita shi da biyayyar addini.**

**(105) Kuma ya umurce ni da in daidaita akan addinin gaskiya, in tabbata a kansa, in kaucewa duk wasu addinai sai shi, kuma ya hane ni da kasancewa cikin masu yi masa tarayya cikin bauta (wato mushirikai).**

**(106) Ya kai wannan Manzo kada ka kira wanin Allah, na gumaka da sauransu, waxanda basa mallakar amfani ballantana su amfane ka, ko cutarwa ballantana su cutar da kai. In har ka yarda ka bauta musu, to lallai a lokacin ka zama cikin azzalumai, masu qertare haqqinAllah da haqqin kawunansu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Imani shi ne hanyar xaukakar ma'abocinsa zuwa matakai na qoli da jin daxin rayuwar duniya.**

**2 - Babu wanda zai iya tilasta wani ya yi imani, domin wannan yana komawa ne zuwa ga ganin damar Allah shi kaxai.**

**3 - Ayoyi da gargaxi basa amfani ga duk wanda ya zarce a kan kafirci, ya tsunduma a ciki.**

**4 - Wajabcin tsayuwar - daka akan addinin gaskiya da kaiwa matuqa wajen nisantar shirka da vatattun addinai.**

وَإِن يَمْسَسْكَ ٱللَّهُ بِضُرٍّ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَ ۖ وَإِن يُرِدْكَ
بِخَيْرٍ فَلَا رَآدَّ لِفَضْلِهِۦ ۚ يُصِيبُ بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ ۚ
وَهُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ١٠٧ قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدْ جَآءَكُمُ ٱلْحَقُّ
مِن رَّبِّكُمْ ۖ فَمَنِ ٱهْتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهْتَدِى لِنَفْسِهِۦ ۖ وَمَن ضَلَّ
فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيْهَا ۖ وَمَآ أَنَا۠ عَلَيْكُم بِوَكِيلٍ ١٠٨ وَٱتَّبِعْ مَا يُوحَىٰٓ
إِلَيْكَ وَٱصْبِرْ حَتَّىٰ يَحْكُمَ ٱللَّهُ ۚ وَهُوَ خَيْرُ ٱلْحَٰكِمِينَ ١٠٩

آياتها ١٢٣ — سُورَةُ هُودٍ — ترتيبها ١١

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓر ۚ كِتَٰبٌ أُحْكِمَتْ ءَايَٰتُهُۥ ثُمَّ فُصِّلَتْ مِن لَّدُنْ حَكِيمٍ خَبِيرٍ ١
أَلَّا تَعْبُدُوٓا۟ إِلَّا ٱللَّهَ ۚ إِنَّنِى لَكُم مِّنْهُ نَذِيرٌ وَبَشِيرٌ ٢ وَأَنِ ٱسْتَغْفِرُوا۟
رَبَّكُمْ ثُمَّ تُوبُوٓا۟ إِلَيْهِ يُمَتِّعْكُم مَّتَٰعًا حَسَنًا إِلَىٰٓ أَجَلٍ مُّسَمًّى وَيُؤْتِ
كُلَّ ذِى فَضْلٍ فَضْلَهُۥ ۖ وَإِن تَوَلَّوْا۟ فَإِنِّىٓ أَخَافُ عَلَيْكُمْ عَذَابَ يَوْمٍ
كَبِيرٍ ٣ إِلَى ٱللَّهِ مَرْجِعُكُمْ ۖ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ٤ أَلَآ إِنَّهُمْ
يَثْنُونَ صُدُورَهُمْ لِيَسْتَخْفُوا۟ مِنْهُ ۚ أَلَا حِينَ يَسْتَغْشُونَ ثِيَابَهُمْ
يَعْلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعْلِنُونَ ۚ إِنَّهُۥ عَلِيمٌۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٥



**(107) Ya kai wannan Manzo, Idan wani bala'i ya same ka daga wajen Allah, ka nemi a kawar maka da shi, to babu wanda zai kawar maka da shi sai Allah Maxaukakin Sarki, kuma in da zai nufe ka da wata yalwa, to fa babu wanda zai hana ka samun falalarsa, Yana bayar da falalarsa ga wanda ya ga dama cikin bayinsa, babu mai tilasta shi. Kuma shi ne mai yawan gafara ga wanda ya tuba cikin bayinsa, mai matuqar jin qai a gare su. (108) Ya kai wannan Manzo ka ce: "Ya ku mutane, hakiqa Alqur'ani ya zo muku, saukakke daga wajen Ubangijinku. Duk wanda ya shiryu ya yi imani da shi, to amfanin hakan zai koma ne zuwa gare shi, saboda Allah mawadaci ne daga biyayyar bayinsa, Kuma duk wanda ya vata, to fa tasirin vatan yana kansa ne shi kaxai, domin shi Allah, savon bayinsa baya cutar da shi. Ni kuma ba mai gadi ba ne a kanku da zan riqa kiyaye muku ayyukanku, in muku hisabi a kai. (109) Kuma –Ya kai wannan Manzo- ka bi abin da Ubangijinka yake maka wahayinsa, ka yi aiki da shi, kuma ka yi hakuri akan cutarwar duk wanda ya sava maka, daga cikin mutanenka, ka yi haquri akan isar da saqon da aka umurce ka ka isar da shi, ka ci gaba akan haka, har Allah ya zartar da hukuncinsa na baka nasara a kansu a duniya, da kuma yi musu azaba a lahira, in har sun mutu akan kafircinsu.**

## Suratu Hud

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Bayanin hanyar Annabawa wajen tunkarar mutanensu masu qaryata su.**

**Tafsir: (1) Alif Lam Raa. Bayani ya gabata dangane da waxannan haruffa a farkon suratul Baqarah. Alqur'ani littafi ne da aka kai matuqa wajen tsara zubinsa da ma'anonin ayoyinsa, ba zaka ga tawaya ko tasgaro a cikisu ba, sannan aka yi bayaninsu ta hanyan ambaton halal da haram, da umarni da hani, da alqawarin ni'ima da na azaba, da qissoshi da sauransu, duka daga Allah Gwani cikin tsarinsa da shari'o'insa, Masanin halayen bayinsa da abin da zai gyara su. (2) Abin da waxannan ayoyi da aka saukar wa Annabi Muhammadu (S.A.W) suka qunsa shi ne: Hana bayi daga bautawa wani tare da Allah. Lallai ni a gare ku –Ya ku mutane- mai tsoratar daku ne daga azabar Allah in kun kafirce masa, kuka sava masa, kuma mai muku albishir ne da ladansa in kun yi imani da shi, kuka yi aiki da shari'arsa. (3) Ya ku mutane, ku nemi gafarar zunubanku daga wurin Ubangijinku, ku dawo zuwa gare shi ta hanyar yin nadama akan abubuwan da kuka tauye na haqqinsa, zai baku kyakkyawan jin daxi cikin rayuwarku ta duniya zuwa qarshen lokutan ajalinku da ya qeve muku, kuma zai ba wa duk wanda yake da wani qari cikin biyayya da da aiki sakamakon qarinsaa cikakke babu tawaya. Amma in kun kawar da kai, ku ka qi yin imani da abin da na zo da shi daga Ubangijina, to lallai ina ji muku tsoron azabar wata rana mai tsananin ban tsoro, ita ce ranar alqiyama. (4) Zuwa ga Allah shi kaxai makomarku take - Ya ku mutane - a ranar lahira, Kuma shi Maxaukakin Sarki mai iko ne akan komai, babu abin da yake gagarar sa, don haka busa muku rai da yi muku hisabi bayan mutuwarku da tayar daku ba zai gagare shi ba. (5) Ku saurara! Lallai waxannan Mushirikan suna sunkuyar da qirazansu domin su voye abin da yake cikinsu, na shakka game da Allah, saboda rashin saninsu da shi. Ku saurara! Yayin da suke rufe kawunansu da rigunansu, Allah yana sane da duk abin da suke voyewa, da duk abin da suke bayyanawa. Haqiqa shi mai cikakken sani ne, dangane da abin da qiraza su ke voyewa.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Haqiqa alheri da sharri, da amfani da cutarwa, a hannun Allah suke ba waninsa ba. 2 - Wajabcin bin Alqur'ani da Sunnah da haquri akan cutarwa da jiran taimako daga Allah. 3 - Ayoyin Alqur'ani cikakku ne babu tawaya ko shirme a cikinsu, kuma an kai matuqa wajen fayyace hukunce-hukunce a cikinsu. 4 - Wajabcin gaggawa zuwa ga tuba da yin nadama akan zunubai, domin biyan buqata da tsira daga abin tsoro.**